da sauri ya zare Écouteur (earphone) da yake ƙoƙarin sakawa yace " me kika ce..,

kai ta shiga girgizawa tana ja da baya jin tayi taci karo da mutum kafin ta gama tantance wa taci karo dashi taji an zabga mata mari da sauri ta dafe kuncinta ta kurawa wacce ta mare ta ido ko kifta wa ba tayi a cikin fusata ahlam tace " chérie (honey) a ina ka samo wannan bagidajiyar wallahi ina upstairs na hango ku ban san ma na sauko ba , bana iya ganin gaba na.,
ahlam ta fadi haka cikin tsananin zafin kishi tare da tallafo habar juraij.
hannun ta ya sauke ƙasa ya riƙe be yi magana ba ya fara tafiya kin binsa tayi tace " magana fa nake maka kayi shiru badai da kaje sabon gari ba suka aura maka ita..,
murmushi yayi yace " aahhlam wallahi ina tsoran randa kishin ki zai illatar min dake, ko dan abin da ke tare da ke ya kamata ki rage damuwa zuwa tayi hutu..,
ajiyar zuciya ta sauke tace " wallahi juraij zan iya kisa akan ka duk randa wata tayi gigin shigowa rayuwar mu to sunan ta gawa na yarda na ƙarshe rayuwata a prison da ka auri wata..,
bata ƙarasa ba taji saukar sanda a dokin huyan ta durkusa'wa tayi ta saki wani irin wahalallan ihu..
juraij da ya shiga wani hali a riki ce yace " sweet me ya faru badai cikin bane na shiga uku ya Allah, duk tattalin da na ke yiwa wannan abu kar ace zu bewa zai yi..,
da hannu tayi mai nuni domin bata da bakin magana ɗagowa yayi ido hudu sukai da yumna tana murguda baki tare da cin ɗamara da mayafin'ta tace " ce miki akai jaka ce tayi yaye ni da zaki dake ni ku da tattabaru sarkin aure ko to wallahi duk wanda yayi min ba zan raga mai ba ai ba jaka aka kawo miki ba , Allah ya saka mazalkwaila ce uwar alawa kuma idan baki sani ba ki sani yau aka ɗaura mana aure sai ki mutu  dan kishi..,
sakar baki juraij yayi yarinyar ta soma ba shi tsoro yawa aljana kai anya kuwa kanta ɗaya dole ya koya mata hankali shu'umancin'ta yayi yawa dole ya tauna tsakuwa domin a'ya taji tsoro a fusa ce ya taso yayin da ahlam ta zun duba ihu  ta danƙi huyan, yumna.
duk karfin yumna kasa kwace wa tayi da ga rikon da ahlam tayi wa wuyan ta zaro ido ta din ga yi
idon ahlam ya rufe babbar buƙatar taga ta kai yumna kasa , taga  ko motsi ba tayi cikin ɗaga murya tace " wallahi ina gamawa da ita kanka zan dawo daman ni naji a jiki na wannan yarinyar zaka auro ka kawo ta Cikin gida na to wallahi Allah ahlam daka kai har ita yau sai na koya muku *DARASI* wanda ko gaba aka ce ka ƙara gigin kawo min wata cikin gida na ba zaka ƙara ba...,
Mommy da yusra suka fito cikin tashin hankali saboda me bawa shukoki ruwa ya je ya faɗa musu ahlam zatai kisa dakyar mommy ta karbi yumna a hannun ahlam yumna kuwa zubewa tayi a ƙasa tana farfari da idanuwanta zata tada aljanun karya ganin hankalin kowa yayo kanta ta maƙe murya tace " wallahi ba zamu yarda ba , ni turkwa dan gidan Sarkin aljanu zata shaƙewa wuya to yasin sai na kwashe mata hanjin cikin ta tas...,
ahlam tana jin wannan magana ta ɗora hannu akan ta , ta zunduma ihu gumi duk ya karyo mata ba ƙaramin tashin hankali ta shiga ba da jin wannan zance shikkenan unborn din su zai dena rayuwa itama tasan mutuwa za tayi ƙara shiga wani hali jin surutan da yumna ke yi.
Mommy kuwa rasa me yake mata dadi tayi ta kalli juraij tace " juraij dan Allah temaka ka dauke ta ka kaita parlour muyi mata addu'a ko a samu ta dawo dai-dai...,
ƙara lankwasar da kai yumna tayi ta mai da hannayen ta baya tace " yasin kana ɗaga kafar ka sai na cire maka jijiya ɗaya a wuyan ka ka dena motsi na tsawon shekaru goma sha biyar..,
cikin fusata juraij yace " ke zanci ubanki idan baki dawo dai-dai ba mu za kiyi wa Prétendre (pretending ) zan babɓallaki idan baki tashi ba.,

sandarewa tayi ta mimmiƙe tare da miƙe hannayen ta tace " yau zaka ga me zai faru dole su aljani tsifur su tafi dakai..,
mommy tace " juraij bana son wauta karka sake ka ƙara cewa ƙala ka tafi gidan liman ka kirawo shi..,
bece komai ba ya juya yumna najin haka ta dinga sakin atishawa zunbur ta tashi tace " mommy jikina ciwo yake min..,
mommy kamo yumna tayi ta rungume ta tace "sannu Allah ya baki lafiya.."
ɗagowa tayi ta kalli mommy tace "me ya faru..?ni lafiya ta qalau...,
tausayin ta ne ya ƙara kama ta , mata tace " bakomai tawo mu je ki ci abinci kiyi wanka...,
washe baki yumna tayi ta juya ta dauki kayan ta , tace muje mommy..
mommy tace " yusra kuje parlour ke da ita ina zuwa juraij tsaya..,
to yusra tace ta riƙe hannun yumna suka shiga daga ciki kallon ahlam tayi da har yanzu ba ta dena kuka'ba tana shafa cikin'ta takaicin tane ya kama mommy tace " ahlam sai kiyi shiru tunda komai ya lafa me ya faru..,
ba kunya ta rungume juraij tana kuka tace " wancan sandar ta dauko ta buga min a kafaɗata haka kurum kuma ashe juraij cin amanata yake wallahi ba zan yarda ba sai ya sake ta ko kuma na cire mata wuya..,
cikin mamki mommy tace " kanki ɗaya kuwa kinsan me kike fadi..? wa za ki cirewa kai ..?,
dukan kirjin juraij ta fara tana wani gunjin kuka riƙe mata hannu yayi yace " ahlam kanki ɗaya kuwa..? karya take fadi..,
a fusace tace " kai na dubu ba ɗaya ba daman kana da kunyar da zaka iya kallon idanuwana ka faɗa min haka...? to yasan ka jawa kowa na gidan nan sai na kona yarinyar nan..,
mommy danne zuciyar ta tayi domin a ƙaramin takaicin halin ahlam take ba , ta mai da kan'ta yawa ' wata naga akan kishi bata ji bata gani tace " juraij wai me yake faruwa ne ka tsaya ka zama gunki..,
cikin takaici yace " wannan yarinyar ce tace mata wai an daura mana aure Ita kuma batare da dogon bincike ba ta soma kuka shine fa ta shaƙe mata wuya..,
wacce yarinyar mommy ta tambaya cikin tsare gida ban da rashin kirkin juraij sunan yumna ne ba sani ba kome.
da sauri ahlam ta kalle ta tare da share hawayen ta tace " mommy sannu da zuwa..,
kai mommy ta dauke tace " yauwa..,.
tare da juyawa ta bar gurin.
ahlam kallon sa tayi tace " baby bazan iya zama ni kaɗai ba dan Allah karka fita kana dai ji abin da aljanunun nan suka ce ko dan girman Allah karka fita.,
kai ya girgiza yace " ahlam kardai ki ce min kin manta abin da kikai min yanzu..?,
turo baki tayi tace " kai hakuri..,
kama hannunta yayi be ce mata komai ba suka soma tafiya kai tsaye shashin su , suka nufa,
zama juraij yayi yace " ahlam yunwa nake ji me kika dafa..,
zama tayi tana kauda kai tace " ni ba abin da na dafa bana son jin kamshin abincin dan Allah idan kaga yusra tayi abinci nima sai ka samamamin na dan samu naci yunwa nake ji tun safe da kai mana breakfast ban ƙara cin komai ba.,
bece komai ba ya tashi yace " ki haɗa min ruwan wanka.,
turo baki tayi tace " beb nagaji wallahi yarinyar nan duk ta wahalar da rayuwa ta Please kai

hakuri karka ce kana ta saka ni aiki ban yi ba nasan ba zaka ji dadi ba...,
juyawa yayi ya shiga bedroom yana shiga ta kwanta ta ɗauki wayar ta , taci gaba da kallon ta a YouTube.
Wannan kenan
yumna tana shiga main parlour gidan ta nemi guri ta zauna tare da ɗora kafa ɗaya kan ɗaya a zuciyar ta cewa take ina ma wannan gidan nata ne , Allah dai ka kaita makkan nan ta kwashi arziki ta barshi a mazaunin sa.
ga abincin naki yusra ta fadi tana ajiye mata tray a kan center table.
da sauri ta sauko ta zauna tare da sauke tray din ƙasa tace " Nagode..,
ya tsuna fuska yusrah tayi ta dauki remote ta zauna ta chanza channel.
taɓe baki yumna tayi tace " halin ki ɗaya da wanki..,
da sauri yusrah ta juyo tace " ke magan kike..,
shinkafa yumna ta watsa a bakin ta tace " ah waka nake..,
ke dan ubanki ni kike faɗawa haka kaga shegiyar kauye..,
yusrah ta faɗa tana yowa kan yumna.
juya idanuwan'ta yumna tayi tace " ina matsowa sai na hanaki kashi na tsawon kwana takwas tare da ciwon ciki me tsanani..,
Chak yusra ta , tsaya gaban ta ya fidi yace rass dafe kirji tayi ta bar gurin tane cewa juhud juhud juhud.
juhud fitowa tayi tace " lafiya yusrah kike kirana yawa wacce na ci miki wani abin..?,
wallahi juhud mun shiga uku mommy ta kawo mana annoba cikin gidan nan.
cire glasses din'ta tayi tace " annoba kuma a ina ..?,
zama tayi akan wasu kujeru da suke jere a gurin farare tas dasu gwanin sha'awa tace " wallahi annoba yar gidan aunty halima..,.
tunani juhud ta shiga yi domin ta dade ba'a kasar ba sannan koda can bata shiga sabgar mutane balle yanzu da ta taka wani matsayi me girma aiki take yi a babban Company wutar lantarki tace " wace aunty halima ke ba'a raba ki da kwashe kwashe ke da mommy halin ku ɗaya wallahi..,
sister din mommy fa
dafa goshin ta tayi tace " wallahi na manta ikon Allah ita tazo ..? da kike cewa annoba aka kawo mana akan ki zata zauna ne yusra ki deba abin da kike yi wallahi haka kurum ki dinga damun kanki da damuwar mutane..,
Ya Allah ya juhud baki fa ki tsaya kin ji me zance ba kin hau faɗa.,
sarke hannuwanta tayi a kirji tayi " oya faɗa min ina sauraren ki..,
bata labari ta soma yi tun daga farko har karshe.
dariya juhud tayi tace " wallahi kun ban dariya da ilimin ku da komai ku tsaya ana raina muku hankali dama mom ta bar big bro yaci uban'ta gaba ko ce mata akai tayi wallahi ba za tai ba karya ne ba wani aljanu yanzu ke saboda ta faɗa miki haka shi ne kika tawo nan kafin ta hanaki kashi right..?,.
cikin matsanancin tsoro yusra ta gyaɗa mata kai
murmushi tayi tace " jeki ki dauke shegiya da mari zata fahimci nan ba can bane..,
cikin kwarin gwiwa yusra ta tashi juhud tace " yauwa ta gida na idan da hali ki dauki tray din da kika kai mata abinci ki kwaɗawa shegiya ni wallahi bana son irin wannan rainin hankalin.,

to kawai yusra tace mata ta sauka ƙasa samin yumna tayi ta zauna sai zuba uwar loma take yi damarar ma da taci da mayafin'ta ta kunce ta ɗan acewar ta wannan damarar da taci hanata sakewa za tayi gwara ta sakata ta wala ta fararraje gidan mommy ne taci duniyar ta da tsinke.
kaza ta dauka taci ta limshe idanuwan'ta wani dadi na ratsa mata jijiyoyin jikin ta ga sanyin AC kai jama'a dole ta nemo arziki dole ta tashi tayi faɗa da talauci miƙe ƙafafuwan ta tayi tare da harde su guri ɗaya tana sakin gyatsa
karasa gyatsannan ke da wuya ganinta ya dauke na wasu da kiƙa sakamakon marinta da yusra tayi tace " dan ubanki wa za kiyiwa karyar aljanu Allah ya saka kukar bulukiya ce aka ce ki , ki bini a hankali kar kafin ki tafi ne sauya miki halitta..,
yumna ba tai wata wata ba ta sunkuya kamar be neman wani abu ta kama diga digin yusra ta gartsa mata cizo.
kasa koda motsi yusra tayi banda ihu ba abin da take mommy ce ta fito da sauri tana cewa me kuma ya ƙara faruwa...?
karaf a kunnen yumna sakin jikin'ta tayi tana mimmiƙe'wa kamar yadda tayi a dazun nan mommy tace " yusra me kuma ya daki da ita yusra wallahi kike yaye ni be kamata ba ki kulata kome tayi miki tun da kunga ba hankalin ku ɗaya ba kin girmeta ga kuma wannan lalurar da take yi dan Allah yusrah ki dinga sara kina duban bakin gatari.,
dakyar ta iya zare kafar ta , ta zauna tana sakin ajiyar zuciya tace " mommy rashin kunya tayi min fa...,
kwafa mommy tayi ta durkusa ƙasa ta ɗago yumna ta ɗora ta akan cinyar ta tana yi mata addu'a atishawa tayi ta dawo dai-dai da yake uwar hanjinta, ta dauka gyara kwanciyar ta tayi nan da nan bacci ya dauke ta..,
cikin tausayi mommy tace " dan Allah yusra kome za ta faɗa miki kada ki kalle ta ni wallahi bansan tana da aljanu ba , Allah sarki malam shi kuma irin kaddarar sa kenan.,
turo baki yusrah ta yi tace " yanzu mommy ko haka zan zuba ido tai ta gasa min magana son ranta..?,
a'a yusrah biye mata ku raba abib fade, shi dai aljani ba kamar mutum bane jeki,
ki kirawo juhud ta zo ta gyara gurin nan saboda idon ki ya rufe ga yadda kuka zubar da abincin nan .
mommy bazan iya tashi ba ina jin kashina ya karye wallahi kafata wani irin zugi take min.
08141785374
09061890481
Only charting

copy is not allowed
https://youtu.be/WoCX8WbJOuU
Episode 6
Yumna tace " mommy ban koshi ba...,
tashi mommy tayi tace " to bara na karo miki idan baki koshi ba sai kiyi min magana...,
washe baki yumna tayi zuciyar ta fari kal tace " to nagode mommy..,
wata uwar harara yusra ta banga mata itama yumna ta mayar mata ita mommy kuwa girgiza kai tayi ta shiga kitchen juraij ne ya shigo yace " yusra me kuka girka ne ki zubo min...?,
share kwalla tayi ta nuna yumna da yatsa tace " ga mommy nan zata je ta ƙaro mata abinci

yawa jaka dan baka ga abincin da dazu na zuba mata ba kaga yadda ta zubar yawa me bulallan baki..,
Zama yayi akan ɗaya da kujerun parlour kallon mamaki yake mata yace " wannan plate din ta cinye dukka kuma take neman ƙari to wallahi ba zata ci ba yau sai taci uban'ta a cikin gidan nan...,
tashi yumna tayi ta murguɗa baki tare da daukan jakar kayan ta tace " dan kunga bani da gata shine kuke zagin mahaifina, to wallahi bazan zuba ido ba nan da kuka ganni na iya rashin mutunci buhu buhu yasin zan maganin ku..,
sakar baki yusrah da juraij sukai kwafa juraij yayi ya maida hankalin sa kan wayar sa yana dannawa ganin fitowar mommy.
mommy kallon yumna tayi tace " yumna lafiya na ganki da jaka..,
kuka ta fashe dashi ta saka mayafinta tana kare fuskar'ta tace " mommy gwara na koma garin mu tunkafin abin ya gangaro kan mahaifiyata da take ƙasa yanzu wannan mutumin zagar malam ya gama yi.,
salati mommy ta saki tace "juraij da hankalin ka..?,
ɗagowa yayi kamar be san me yake faruwa ba yace " mommy me ya faru yanzu na shigo aka ce kina parlour ban dade da zama ba..,
kuka yumna ta ƙara fashewa dashi tace " kallo yadda yayi maganar kamar be san abin da sukai ba wallahi mommy ya zagi malam..,
Kiyi hakuri dauki abincin ki zau dauki babban mataki akan su ɗauka tayi ta nemi guri ta zauna a hankali take cin abincin dan ta tura wa juraij haushi tashi yayi ya fita, be jima ba ya dawo huce wa yayi ta gaban ta da sauri ta ɗauke abincin ta sakamakon kyankyaso da ya saka mata kuka ta fashe dashi ganin irin abin da yayi mata gashi ko rabi bata ci ba.
mommy ce ta fito take tambayar ta lafiya shiru tayi tace " bakomai na koshi..,
Kallon yusra tayi da har yanzu take zaune tace " ya kafar taki ta samu sauki..?,
ajiye wayar ta tayi tace " eh na samu sauki..,
zama tayi tace " yauwa kikai yumna dakin ki, tayi wanka ta kwanta bacci ta samu hutu..,
da sauri juraij yace " mommy kawai ta zauna a part dina kinga ahlam ta Dan samu me debe mata kewa idan bana nan..,
ba ƙaramin dadi mommy taji ba domin ko ba komai ya nuna cewa yumna yar uwar sa ce kuma ahlam zata ɗauke ta da mahimmanci batare da ta kawo komai a ranta ba tace " okay ba damuwa yumna bi yayan ku part din sa ...,
da sauri yumna ta kalli mommy ita dai wallahi ko rantsaiwa za tayi ba za tayi kaffara ba akwai abin da ya shirya amma koma mene ita dai-dai da su take daga shi har matar sa me katon kai tace " to mommy yaya taso nagaji wallahi..,
sakar baki yusrah tayi to me yaya yake nufi da yin haka daga shi har matar sa basa son hayaniya barin yanzu da take da ciki a jikin ta sai taɓara take mai yana dada shagwaɓa ta yawa yar kwai baya san damuwar ta ko yana gun aiki ta kira shi sai yaje ba kuma ta buƙatar wani ya zo mata dan kishin masifa ne da ita tab lallai za ayi ta ta fadi cikin ranta tare da tashi tabar gurin.
bin bayan sa yumna tayi yana gaba tana binsa a baya har suka isa part dinsa ahlam da take kallo da sauri ta tashi zaune tana yi mai kallon tuhuma ga hannun sa na dukan cinya ba abinci cire earphone tayi tace " sweet wannan fa me tazo tayi min Avant que ma colère ne s’aggrave,

j’ai dit quelque chose que je n’avais pas l’intention de dire, alors elle a quitté l’endroit..,
zama yayi kusa da ita ya kamo hannun ta ƙasa ƙasa yace" na kawo tane ki rama abin da duk tayi miki ita zata dinga komai yanzu ma ki faɗa mata me zata girka..,
ahlam uwar son jiki tuni ta washe baki ta yi mai kiss a kumatu dauke kai yumna tayi tana jan ƙara min tsaki abin nan yana baya haushi wallahi ashe daman yan iska ne ga abin da suke yi yawa za su cinye junan su ta faɗa ƙasa ƙasa da sauri juraij ya juyo domin tas yaji me tace , dan haka tashi yayi yace " su waye yan iska..?,
yadda yayi maganar cikin i don't care manner ba ƙaramin shakkar sa taji ba sai taga ya koma mata wani iri ja da baya tayi tace " ni ban ce komai ba baiwar Allah dan Allah kin ji nayi magana..,
tashi ahlam tayi tana gyara zaman rigar'ta tace " karya take tayi magana, naɗa mata na jaki ba ɗazu mu zaki rainawa hankali da aljanun karya to ina me sanar dake kin zo inda za'a gyara miki zama da hallacan jeki kitchen ki dafa min tuwan shinkafa miyar ɗayar kuɓewa..,
kallon sa tayi tace " ba cewa tayi ba nayi wanka na kwanta na wuta..,
ta fadi haka tare da gyara zaman ledar kayan ta ..,
ƙara shan toka yayi yace " kafin na kirga uku ki tafi kiyi abin da ta saka ki ko jikin ki ya faɗa miki..,
fakar idanuwansa tayi ta fita a kuje sai dai gate a rufe yake ba ta yadda za a yi ta fita.
juyowa tayi tana yana haɗe hannun riga daman gashi ingarmar namiji sako sakon da yake mata shine har ta samu damar ya faɗa ta bashi amsa amma yanzu zai saita mata kan'ta.
ɗurkusawa tayi da ledar kayan ta tace " dan girman Allah kayi hakuri..,
ke kin san shi ne..?
ɗago kan'ta tayi ta kalle sa idanuwanta tab da hawaye tace " dan Allah ba danni ba karka dake ni kaga ni marainiya ce...,
tsawa ya daka mata yace " shige ki tafi kiyi abin da ta saka ki...,
to tace ta tashi tana daɗa rungume kayan ta wayar tace tayi ringing da sauri ta buɗa ledar ta ta ciro ta sunan Mamman ta gani dogon tsaki taja tare da mayar da ita cikin ledar ta.
dan ubanki wa kike wa tsaki...?
da sauri ta juyo tace " gidan layi ne suka kira ni shine nayi musu tsaki. ..,
bake bakin ta yayi yace " mara kunya su din sa'an wasan ki ne..,
girgiza kai tayi tace " kai hakuri nadena..,
yaro besan wuta ba sai ya taka tabbas za tayi maganin su ta fadi haka a cikin zuciyar ta , tana shiga ta ajiye kayan ta , tace " ina ne kitchen din..?,
wani banza kallo tayi mata tace " gashi nan sauran naga ba dai-dai ba..,
leƙawa tayi tace " ban iya amfani da wannan abin ba sai kin koya min..,
tsaki taja tana tashi ta shiga kitchen din bin bayan'ta tayi ta tsaya juyowa tayi tace " kalli bana son dakiƙanta sau ɗaya nake magana na biyu sai dai kiji duka..,
zumburo baki tayi ranta yayi ba dad'i baya kaunar hulakanci ta ɗauke kanta ji tayi kamar ta dauki  fry pan ta buga mata akai sai wani juya mazaunan ta take .
ke ina magana kina tunani to wallahi mijina da gidan nan yafi karfin ki.
murmushi yumna tayi tace " da ace ina son shi da be aure ki ba tunda ko ba komai wata kusan tafi wata da arziki a garin wasu gwara a garin ku acikin dakin ku dan uwa dan uwa ne mijin ki baya gaba na da ace ina son sa ina me tabbatar miki da wallahi ko za kiyi hauka sai na aure shi

ki godewa Allah yanzu ba kune agaba na ba , akwai abin da yafi ku mahimmanci...,
Kut lallai yarinyar nan ta fadi haka tana dauke ta da mari sai dai yumna ta kauce ta ja da baya tace '' ke waya faɗa miki yanzu ana yayin yar doke doke wannan sai karurnuka da karya ki godewa Allah da ba a zamanin da wannan abin ya faru ba da nayi tsalle na duro akan ki na bawa hammata iska naci kutumar ubanki hankali kwance..,
kasa magana ahlam tayi sai nuna yumna take yi da yatsa lankwasa yatsan tayi tace '' la la lah ba'a nuna ni da dan yatsa ban tauna shegeba kinyi sa'a ɗaya ke matar yaya ce da yau hmmm sai dai wani labarin hajiya ta...,
Sweet sweet sweet kana ina kana ina zo kafitar min da yarinyar nan tun kafin naci uban'ta...,
da sauri ya shigo daga shi sai towel shaf ya manta da yumna a cikin gidan da sauri ta dauke kan'ta tana cewa a'uzubillahi..
kaga ko daga shugowar ka tana maka ta'awizi ga babban sheɗan ya shigo kaga irin maganar da ta faɗa min kasa komai nayi dan haka kai kazo ka naɗa mata duka ka nuna mata matsayi na a gurin ka..,
Ahlam ta faɗi tana ɗauke kan'ta daka kallon yumna.
ran juraij ne ya ɓaci domin baya son yaga ƙaramin yaro yana raina babba haka kurum ya ƙara jin tsanar ta ta sami guri a cikin zuciyar sa yowa kan'ta yayi ya zabga mata mari ai wasu taurari ta gani ta faɗi a ƙasa bakin ya fashi yace '' ki tashi kuma ki girka mata abin da tace miki idan ka yi mata ba nan ma jikin kine zai gaya miki...,
jikin ta rawa ya fara ta miƙe tace '' banga kayan aikin ba , ban iya kunna wannan abin ba..,
ta faɗa tana nuna gas..
kunna mata ahlam tayi ta kama hannun mijin ta suka bar gurin kuka yumna ta fashe dashi ko a gidan su ta manta yau sharabon da tayi girki da kan'ta ta nemo komai tayi wa ahlam girki bayan ta gama ta zuba a plate takai mata.
tana kwance akan cinyar sa a hannun sa wani story book ne yana karanta mata daga shi sai boxer ita kuma wasu English wears ne rigar iya gwuiwa ba wando kenan wanka tayi haka ta raya a zuciyar ta ajiye wa tayi a inda taga yusra dazu ta ajiye mata abinci..,
zama tayi a gajiye tace '' gashi na gama..,
ɗagowa ahlam tayi tace '' oh tashi to ga can dakin nan ki dauke wa'yannan kayan naki tun da kika ajiye dakina yake wari..,
ɗauka tayi bata ce komai ba ta shiga dakin da ta nuna mata zama tayi akan dan madaidaicin gadon dakin komai akwai har da wardrobe.
fito da wayar tayi ta yiwa Mamman Flashing.
ba jimawa ya bugo yace '' masoyiya ashe kin yi tafiya shine ba sallama..,
juya idanuwan'ta tayi ta maida su dai-dai ta taɓe baki tace '' oh na manta ne yanzu dai turo min kati zanyi waya da kawata..,
shiru tayi ta saurara domin taji me zai ce kwanciya tayi tace '' kadai ce min ba zaka turo ba amma wannan kwana kwanar da kake yi ban gane mata ba gwara ka fito fili ka faɗa min yumna bazan turo ba..,
kwantar da murya yayi yace '' yumna bani dashi ne wallahi amma zan ranta na turo miki..,
kashe wayar tayi tana jan ƙaramin tsaki kwanciya tayi sosai saboda ɗazu kawai ta kishingiɗa ne tane cewa katin fcfah 1000 ya gagare shi haba Allah ina neman tsari da talauci dukka abin da Allah da manzon sa suka ce ka nemi tsari da shi ba karamar masifa bace haba talauci ai dan

ta'adda ne lokaci ɗaya yake maka kaca kaca ya sauya maka kamannin ka ni yumna da auren Mamman aha ai kwai wannan auren shi ake kira da auren manufa ko wata bazan ba , zan fito daga nan kuma sai makka ina da yancin yin komai ina da yancin aurar wanda naga dama.
YAN ZAMAN MAKKAH
domin fara paid na wannan littafin zaku biya ₦500
0423988701 amina Alhasan Muhammad wema bank
Ko
8141785374
Amina alhasan Muhammad opay
ku turo da sheda tanan 08141785374
Yan niger kuma
Zaku turo da kudi ta my nita 1000fcfah
da shedar biya ta wannan number 08141785374

copy is not allowed
https://youtu.be/WoCX8WbJOuU
Episode 7
ɗaga wayar ta tayi tana kallon ta ko zata ga sakon kuɗin can sai ga alert ya shigo wani dad'i ya kamata ta , tashi zaune tace " ihuu huuu bara na kirawo na'ima..,
tana wannan maganar sai ga kiran sa ya shigo tsaki ta ƙara ja ta ɗauka tace " naga ni Nagode sosai Allah ya ƙara budi..,
jin dadin addu'ar ta yayi yace " wallahi yumna idan ina da shi ba abin da bazan miki ba kedai Allah ya saka noman mu yayi kyau kar fari ya mamaye mana gona akuya zan siya miki na dira miki kiyo lokacin da bani dashi kinga zaki siyar kiyi abin da kike so..,
da sauri ta miƙe ta dafe kirjin ta lallai sai yau ta kara tabbatarwa wanda yayi nisa baya jin kira ita da kiwo amma dai ba'a ƙin ta mutun ko wani abin tayi da kudin mugun fatan sa kuma ya koma masa kansa ɗan uwar ubansa tace " uhmm amma dai ni zaka bawa na siya ko sai na zabi kalar da nake so.?,
ai masoyiya tare za mu je ki zaɓa ki darje har da dan bunsuru zan siya kinga mun haɗa aure ɗaya..,
zaro ido tayi sai kuma ta danne zuciyar ta , ta yayyafa mata ruwan sanyi tace " eh haka yayi sai anjima zan kirawo ta karta ga na hulakanta ta..,
to ki wuta lafiya abar kauna'ta wani takaici ne ya tokare mata zuciya hmmm zatai maganin sa very soon.
zare wayar tayi ta kashe ba tare da tace komai ba number na'ima ta kirawo sai dai har ta gama ringing bata ɗauka ba dogon tsaki taja ta ƙare kira amma nan ma ba'a dauka ba sai dai da ta kirawo ta har sau biyar kamar wata mayya ta kasa haƙura.
sai da taga ba sauki ciwon arne ta hakura ta ajiye wayar zuciyar ta na tsalle babban burin ta , ta kirawo na'ima su gama wannan maganar a saka mata date din tafiya insha'Allahu ba zata basu kunya ba.
ji tayi anyi knocking dib kofar dakin da take da sauri ta tashi ta bude domin taɓa kyautata zaton wa'yannan yan wahalar ne aikuwa ilai ahlam ce kallon ta , tayi tana yatsuna fuska tace " ki fito ki kwashe kayan da nayi amfani dasu sannan nayi baki zaki kawo musu Boissons (drink's) da

friandise (snack) sauran kuma ki musu rashin hankalin da kika saba kar kuma ki nuna kina da alaka da me gidan saboda abin kunya ne a gare shi..,
da sauri ta ɗago jin karshen zancen ta zaro nata kananun idanuwanta tayi masu kama dana yan chaina tace " karya nayi ke ba abin kunya ce a gare shi ba fitsararriya mara kunya..,
bata nuna mata taji haushin maganar ta tace " oh amma dai baza a iya canza wa tuwo suna dole ace da mijin iya baba..,
wani mijin sunan sa muna miji saboda baza a iya nuna shi a ko wanne waje ba , ba zai iya zame maka wata babbar ƙaddarar ba.
wani yawu me ɗaci ta hadiya jin zancen ahlam amma ta cita wasa binta tayi da kallo har ta juya sai kuma ta dawo tace "ki canza kayan nan na jikin ki, ki kuma saka hijabi..,"
ɗagowa tayi tace " bani dashi ko kin siya min ne..?,
dariya tayi cikin salon tura haushi tace " a'a amma dai a matsayina na wacce take amsa sunan matar gidan nan dole kibi doka ta ki zauna lafiya..,
gani tayi mene amfanin ta tanka mata banga je ta tayi ta fita sakar baki ahlam tayi ganin baki sai kuma ta saita kan'ta kallon bakin tayi ba hausawa bane turawan France ne.
gaishe da su tayi suka amsa cikin sakin fuska.
kwashe kayan da ahlam tayi amfani dashi tayi takai kitchen buɗe fridge tayi ta dauko lemuka da kayan motsa baki ta saka akan tray ta kawo musu sai yanzu ta lura ashe har da bakar fata tana tunanin duk yadda akai ba dan nan bane saboda hausar da yayi amfani da ita gurin cewa mun gode sannu da aiki da ga gani dan Nigeria ne murmushi tayi har beautiful point dinta ya loɓa tace " bakomai wallahi bisimallah..,
dariya yayi yace " amma dai nawa kason yafi na kowa ko..?,
da sauri ta kalle sa tace " eh naka ne duka..,
daukan lemo ɗaya yayi yana kallon ta tace " really..?,
kai ta ɗaga mai wani takaici ne ya kama juraij da ahlam su kuwa sauran sai dariya suke dan haidar ya iya barkwanci sosai gwanine gurin wannan baya barin waje tsit..
har tayi nisa yace " baki gama aikin ki ba..,
yumna bata da duhun kai dan haka ya juyo batare da wani kauyenci ba tace " to ina sauraron ka me kake so..,
DO YOU LOVE ME...?,
da sauri ta kalle sa kaɗan kaɗan tana Ingilishi akwai wani malami da yake dan koya musu dan haka ta fahimci me yake nufi zaro idanuwanta tayi tace " ka taɓa ganin jin inda musulmi yaƙi dan uwan sa musulmi..?,
Haidar yace " right amma ni ba irin wannan nake nufi ba..,
Juraij ne yace " ke tafi daki..,
shiga tayi daki kirjinta yana lugudan uku uku duk abin da take karfin hali ne zama tayi tai tagumi murna za tayi ko kuka garin dad'i yana nesa ta tabbatar daga ganin wannan mutumi be san talauci ba duk da ba lallai ne ba ya kai ya juraij. anya kuwa ma zai bari saboda tasan halin su sarai shi da matar sa me kan tasa tsaf zata iya wargatsa abin.
to amma fa ya za tayi Mamman to hakan yana nufin mafarkin ta da burin ta ba zai cika ba wannan mutumin fa bata iya tai mai abin da zatai wa Mamman ya sake ta ba tun da wayewar ba ɗaya ba wayar tace tayi ringing da sauri ta ɗauka ganin kiran na'ima tace " na'ima ke kuwa kina ina ..? nake ta kiran wayar ki amma baki dauka ba kira har biyar ki bacci kike ya kamata

ace kin ɗauki wayar nan..,
cikin raɗa da rawar murya na'ima tace " cikin tsakiyar dare zan kira ki yanzu ina aiki ne dan Allah yumna karki kirani zan kira ki..
kit ta kashe wayar bata jira me zata ce sauke wayar tayi akunne tana kallon screen din wayar to me yake faruwa jin muryar ta tayi kamar tana cikin wani hali
cikin dare zata kirata kenan bata da yancin ɗaga waya a lokacin da taga dama kuma tayi niya.
Sai wanda aka dibar mata da sauri tace " zato zunubi ko da ya kasance gaskiya ban dai san me ke faruwa ba wannan tambayoyin nawa bani da me bani amsar su..,
Tana cikin wannan tunani ahlam ta shigo wani kallo ta wurga mata yace " ke Wallahi kibi a sannu kafin na rugurguza miki kasusuwan ki dan rainin hankali daga ganin baki sai ki dinga wata kwarkwasa kina canza salon tafiya ke gaki me neman miji ko...?,
Dariya yumna tayi irin ta rainin wayon nan tace " nai miki kama da wacce za'a kasa a fefe ana tallanta nan da kike gani na yau sauran sati takwas biki nan..,
turus ahlam tayi wani dad'i ne ya rufe mata gwara ai mata aure ta huta ganin yumna a cikin gidan ta zai saka ciwon zuciya ya kamata gashi bata da kunya dai-dai take da ita duk Maganar da ta faɗa mata , tana da amsar bata hakan ba karamin bakan ta mata rai yake ba juyawa tayi ta fita tana jan tsaki.
bacci n yayi awan gaba da yumna me cike da mafarkai kala kala ,
tana cikin wannan bacci taji an maka mata pillowcase da sauri ta tashi tana zare idanuwa ido hudu tayi da juraij da sauri ta ja baya tana dauke kan'ta a hankali ta furta wallahi Allah ya isa ai wannan ba tarbiyar musulunci bace ka dinga yawo da kai sai gajeran wando.
zaro idanuwanta sa yayi ya nuna kansa yace " me kike faɗa ni kike faɗawa wannan maganar..,
sosai tashin ta da yayi ya ɓata mata rai domin mafarki tayi gaba a gaban ka'aba tana sauke farali dan haka ta shi tsaye tayi ta kau da fuska tace " da wanda ya tsargu..dashi nake.,
Kifa mata mari zai yi ta zube a ƙasa tare da sakar wata ƙara da sauri ya toshe kunnuwan'sa saboda jinsa yana barazanar daukewa na wucin gadi.
da sauri ahlam ta shigo tana cewa honey me ya faru lafiya daga ina karar nan take ganin yumna a kwance da sauri ta kama hannun juraij tace " kaga tun kafin abin da yarinyar nan take fadi ya tabbata akan mu, ka mai da ita inda ka dauko ta Please ba danni ba wallahi ganin ta acikin gidana bani da kwanciyar hankali ko kaɗan kai min wannan alfarmar kai daga jin karar nan kasan ba mutum ne yayi ta ba jibi yadda ta sheme a ƙasa tamkar wata gawa ni na hakura da rama abin da tayi min wallahi sweet bakai tunani ba ka kawo ta gurin mu...,
fita sukai suka rufo mata dakin da sauri ta tashi tana dariya tace " waya ce da ni ba niba nima nace dashi ba shi ba wallahi kun dinga haduwa da abubuwa kala kala tunda ku baku san kawaici ba na dinga gasa muku aya a hannu shegu masu kan jimina..,
wayar tace tayi ringing da sauri ta ɗauka tsaki taja a duniya bata taɓa ganin mayan mutum ba sama da Mamman tana ji wai wai ana maye maye to tana kyautata zaton yana ɗaga daga cikin mayun wannan wacce irin bakar jaraba ce ɗagawa tayi tace " haba Mamman ina bacci na ba zaka barni ba na sarara na samu hutu da jin dad'i gaskiya abin da kake yi baya dacewa..,
ɗanne ɓacin ransa yayi yace " kiyi hakuri bansan bacci kike ba na zata kin gama wayar ne kuma yau ina so muyi waya mu dade..,
to kashe zan koma bacci haka kurum kai ba damar kabar mutum ya huta wallahi Mamman idan kana min bita da kullin nan baza mu taɓa zama lafiya ba dan katin da ka turo min ne shi ne sai

na biya shi ta hanyar baka lokacina saboda tsabar cutarwa
be tsaya jin karshen faɗan ta ba ya kashe wayar sa zuciyar'sa na tafasa yace " wallahi ilu yarinyar nan daba dan son da nake mata ba da tuni na rabu da ita kwata kwata bata da kirki... hmmm ni zan faɗa maka wacece ita nida take neman naɗa min duka a cikin gidana har da cewa na fice na basu guri ina fuffuka zan naɗe tabarmar kunya da hauka kai wannan yarinyar kamar jikar aljanu nifa da zan faɗa maka kaji yasin karabu da ita domin wannan ko a cikin gidan ka , baka isa ka faɗa mata taji ba saboda ko a waje ma kuna marmarin juna baka fada mata taji ba balle kun gogu da juna sai abin da yayi gaba wallahi ina jiye maka abinda zai je ya dawo..,
Cewar ilu
Shiru Mamman yayi domin yasan sarai gaskiya ilu ya faɗa amma me ya zaiyi da sonta besan wanne hali zai shiga ba idan har be aure ta ba .
Dariya mado yayi yace " ba zai taɓa daukan shawarar kaba shi yasaka ni ban wahalar da yawun bakina ba shi kansa ta malam da yake uban'ta ba jin maganar sa take ba idan tai maka laifi gun wa zaka kai ƙarar ta..?,
shiru yayi yana kallon kasar gonar sa dafa kafadar'sa madu yayi yace " naga baka da amsar bani amma amsar ita ce babu wanda za ka kai wa karar yumna kowa yana son ya auri mata , tagari ya samawa ya'yansa uwa ta gari ita kan'ta yumna tarbiyyar da akai mata bata dauka ba kana ganin zatai wa ya'yan ku tarbiya a bokina ka yi tunani karka daukar wa kanka ƙara da ki yashi.. domin wallahi yumna ba zatai maka biyayya ba idan kai baka bita ita baza ta bika ba.,
Ƙasa cewa komai yayi duniya tai mai zafi tabbas maganar su haka take amma baya jin zai iya rabuwa da yumna,
CIKIN GIDAN MALAM
yaya lafiya naga kin kasa tsaye kin kasa zaune..?,
Cewar baba lami
zama inna Hadiza tayi tace " komai yana shirin lalace mana mutukar wannan yarinyar ta auri yaron nan mun ƙade..,
cikin rashin fahimta baba lami tace " saboda me kika faɗi haka mene namu kuma aciki shi yaron nan ba wani a bin kuzo a gani ne da shi ba..,
tabbas bashi da wani abin kuzo a gani amma ke kina ganin inhar ta aure shi ba zata bar kowa da kwanciyar hankali ba kinsan dai halin ta ba sai na faɗa miki ba ina tunanin zan yi duk yadda zanyi naga abin nan ya fasu..
Lah yaya karki fara ba ruwanki idone naki da kan'sa zai yanka mata takarda ke kinsa halin ta idan bata zame maka dole ba wa zai zauna da ita ga dukan ya'yan mutane dan ma dai mahaifiyar dai-dai take da ita wallahi ɗiyar Moussa wasa ce wallahi tana yi mata yi mata za tayi auren nan ba wani karko zai yi ba ke dai kawai ki zuba ido zuru ma ta ishi mara ɗa kunya.
inna Hadiza tace " wallahi kuwa shi ya saka naso malam ya rabu da ita kawai a cikin yan uwanta ya bashi wata tun da ita ga abin da ta fadi wallahi na kawo kai naji wannan maganar kisa kinsan yadda zuciyar ta take a bushe zata aikata balle tana da wa'yannan mutanan..
Baba lami tace " Allah ya kyauta amma wannan lamari abin a dage da addu'a ne..,
tab duk wanda ya iya allon sa ya wanke ya sha ni da yiwa yarinyar nan addu'a a'a har bada saidai idan na sako al'ummar musulmi baki ɗaya ta shiga cikin su.
cewar inna hadiza
Nazeefa ce ta shigo tana cewa a she Mamman besan da tafiyar yumna ba ɗazu na hadu dashi

yake tambayar tana ina nace tayi tafiya zuwa arlit ya buga mata waya taƙi ɗauka.
hmmm kinga ko shi yasaka nace ba ruwanki shima yasan me ya aura ai yumna kara da kiyashi ce daukan mara sani amma shi ya dauka shi da yayi rayuwa a gurin malam ga yarana nan kala kala, ya rasa wa zai aura sai ita Allah ya basu zaman lafiya amma wannan zama hmmm
Dariya inna Hadiza tayi tace " gane min hanya lami wai makaho yaso gulma yace gane min hanya..,
zama nazeefa tayi tace " wallahi dan baki ga yadda ya ban tausayi ba halin yumna sai ita..,
Shamsiyya da take cikin daki tace " cewa fa tayi ya turo a karbi kudin sa amma be turo ba wallahi da wuya yumna ta samu me sonta tsakani da Allah sama da shi tayiwa kanta kiyamul laili tabi maganar malam ko dan samin rahamar Ubangiji..,
tab ke kika san wannan idanuwanta sun makance babban burin ta , ta jita ta tafi makka Cewar baba lami.
Dariya shamsiyya tayi tace " hmmm Allah ya kyauta..,
amin suka ce
wannan kenan
Har akai kiran sallar isha tana zuba ido taga kiran na'ima amma ba kiranta ba labarin ta lamarin nan ba karamin takaici yayi wa yumna ba , ta dade a zaune a ƙasa ta zuba ta gumi har juraij ya shigo bata sani ba ji tayi an dunguri ƙafar'ta da sauri ta ɗago suka haɗa ido ɗauke kai tayi bata ce mai komai ba zama yayi yana kallon ta yace " anya kuwa ba wani mugun abin kike saƙawa ba...,
ba tare da ya kalli inda yake ba tace " kasan sau da dama mutane gani suke abin da suke aikatawa shi kowa ke ai katawa dan haka bazan iya yin ja yayya da kai ba tun da abin da ke cikin zuciya ne ya fito fili...,
ja kujera yayi ya zauna yace " magana kike..,
kai ta girgiza bata ce komai ba murmushi yayi yace " ashe ke mara kunyar karya ce da ki mai maita da na tumurmusa ki a gurin nan ba aljanu zaki tayar ba ko abin da yafi aljanu ne sai nayi maganin ki..,
jingina tayi da jikin gano bata ce komai ba ta kifa kan'ta a kan gwuiwar'ta..
tamkar an wullo ahlam haka ta shigo tana sauke ajiyar zuciya a jere a jere cikin sarkewar murya tace " sweet daga shiga toilet sai na neme ka na rasa ashe kana nan..?,
ɗagowa yayi dariya abin ya so bashi kishin ahlam yana bashi mamaki babban temakon da Ubangiji yayi mata shi ne shima bashi da ra'ayin auren mata biyu ita kadai ta ishe shi rayuwar'sa.
tashi yayi yace " mu tafi ko..?,
kallon rashin fahimta take mai tace " me kake yi anan..,
dariya abin ya bawa yumna dan haka tayi dariyar ta son ranta sannan tace " yanzu aunty ahlam dan ya zo guna muna sirri tsakanin wa da kanwar'sa shi ne sai kinji abin da yan uwa suke cewa to sirri ne idan abin ya matso kya ji..,
dafe kan'ta tayi da ya sara mata lokaci guda anya kuwa baza ta cirewa yarinyar nan hakura ba , ya za'a yi ta dinga gasa mata magana son ranta juyawa tayi bata ce komai ba ranta a ɓace tana zuwa parlour ta dauki wayar ta ta shiga bedroom din ta zama tayi tamkar wata yar bori rasa ina zata saka kan'ta tayi anya kuwa bata daɓawa kan'ta huƙa ba anya kuwa bata cuci kanta ba wata mace tana ta yarda ta shigo rayuwar su tamkar wata kububuwa haka , ta tashi ta fita

kitchen ta nufa huƙa ta zaro ta shiga dakin da ita tace " maza kwaso kayan ki,ki bar min gida..,
Ahlam kanki ɗaya kuwa wai me isaka zargin ki yayi yawa ki sani fa baza mu taɓa zaman lafiya ba idan har kina zargi..
wani murmushi tayi me ciwo tace " a gaban ka ta gaggasamin magana amma da yake kai ma munafuki ne kai shiri ka tsuke bakin ka to wallahi ina me sanar dake da babbar murya mijina yafi karfin ki..nafi karfin da na zauna dake a matsayin kishiya ta sai dai yar aiki amma ke baki isa ba nayi rayuwa aure tare da ke ba dan haka maza kwaso kayan ki, ki koma inda kika fito haba buri yayi kama da mutum yarinyar nan har tana da karfin gwuiwar kallon idona ta gasa min magana son ranta kai kasan a inda ka dauko ni dan haka baka isa ka wulakanta tani ba wallahi kayi kaɗan...,

dakyar ya samu ya cire hukar hannun ta yumna ta dake ta kasa koda motsi tasan ko giyar wake ahlam tasha ba zata iya daukar huƙa ba ta caka mata dan haka ta dake fita da ita yayi ta zauna tana sauke ajiyar zuciya tace " mahaukaciyar banza kina wannan haukan wata zata aure shi baki sani ba.
kiran sallar isha akai ta tashi ta dauro alwala tayi sallah bayan ta idar bacci ya kwashe ta a gurin misalin karfe biyun dare kira ya shigo wayar yumna a gigice ta tashi bata , taɓa riskar irin wannan yanayi ba cikin lokacin nan a kira ta ɗan haka sai kiran ya zame mata baƙon abu gare ta.
wastsakewa tayi da sauri sakamakon ganin kiran na'ima ta ɗaga tace " wallahi na'ima naji tsoro kira da wannan talatainin daren tun bayan sallar magariba nake saka ran ganin kiran ki..,
ke wallahi bana samin damar zama ne yakike ya kowa da kowa..?,
cewar na'ima
yumna da bacci ya kauracewa idanuwanta tace " wallahi suna lafiya qalau daman ni da nana ne za mu tawo garin da kike muma mu yi aiki shi ne zaki bani number din agent din ki..,
dam jim tayi sannan tace " wallahi a dai yanzu bani da number sa ban kuma san a ina zan samu number sa ba kwanaki na buga mai taƙi shiga da tana ringing ba'a ɗagawa sai kawai naji haushi na goge number..,
inyeee kin sami duniya dole ki goge number sa yumna ta faɗi tana alyini domin bata san ina za ta sami agent din da zai kai ta makka aikatau ba.
amma yumna zan turo miki address din wajen in har kika je zaki same shi insha'Allahu.
okay turo min ba damuwa sai na bincika.
na'ima tace " amma yumna ba ance an saka ranar auren ku ba to shi mamman din ne zai barki, ki tawo nan..,
hmmm ke dai Allah ya kyauta amma ba jimawa insha'Allahu zan zo nema na nemi arziki dole nima na zama ana sawa dani a sahun manya manyan mata masu faɗa aji ko shekara ɗaya nayi na dawo.
wata ƙara taji da wasu surutai cikin daga murya ta fara cewa na'ima hello hello na'ima me ya faru kit kiran ya katsai sosai ta shiga tashin hankali dan daga jin ihun nan ba na dad'i bane ƙara kira tayi sai dai har ta gama ringing ba'a dauka ba , sai dai bata hakura ba ta ƙara kira sai dai wannan karon a kashe wayar take.
jingina tayi da bango tana tunanin me ya faru haka har na'ima ta saki ƙara kuma taki daga wayar ta ,

karon farko a rayuwar ta da , ta mike ta dauro alwala ta gabatar da lafi'la tare da rokon Ubangiji Allah ya shiga lamarin ta ya cika mata burin ta bayan ta idar ta zauna har akai kiran sallar asuba yadda taga rana haka ta ga dare ana kira ta tashi ta yi sallah ta dade nan ma tana rokar Ubangiji ya cika mata burin ta na tafiya makka Allah karya taɓar da ita.
ya Ubangiji Allah ya saka tayi tafiyar nan a sa'a ta faɗa hannu me kyau hannun da zata sami abin duniya bayan ta idar ta zauna a lokacin kuma ta ƙara kiran number na'ima sai dai har yanzu a kashe take to me yake faruwa ta fara zargin anya kuwa lafiya,
tana cikin wannan tunanin ne akai knocking din kofar dakin ta tashi tayi ta buɗe fuskar nan ba walwala tace " ina kwana..,
shima fuskar sa a ɗaure take tamau ba ɗigon annuri a fuskar sa yace " lafiya kije ki ɗora mana petit déjeuner (breakfast) da wuri nake fita office so bana son ɓata lokaci..,
shiru tayi tamkar me tunani tana sane tayi haka , tayi hakan ne domin ta bata mai rai ilai kuwa sai da ya magantu yace " ke ba magana nake miki ba..,
da sauri ta ɗago tana taɓa kunnen ta tace " oh ban ji ba me kace..,
wani kallo da yayi mata dole ta hadiya sauran zancen ta batare da ta shirya hakan ba miskilin murmushi yayi ya juya ya rufo mata kofar ta ahlam ta zaune akan kujera tana cika tana batsaiwa zama yayi yace " ni zan shirya na fita na siya restaurant domin bazan iya cin kirkin yarinyar nan ba , tun da ke zaki iya sai kici ko ba komai ta sauke nauyin da ni ya kamata ace na sauke tun da ke bakya iya shiga kitchen..,
dauke kai tayi tace " nifa har yanzu ina kan bakana sai ta bar min gida gwara na girka da kai na ko da abin da ke ciki na zai zube..,
da sauri yace " a'uzubillahi da bakin ki kike fadar haka haba ahlam me yake damin ke ne..,
Cutar da ka zaɓa min ita take damuna ban da rainin hankali yarinya ta dinga faɗa min magana amma ko sau ɗaya baka saɓa mata halitta ba sai dai idan akwai wata a ƙasa.
girgiza kai yayi ahlam tayi nisa bata jin kira yarinyar da an kusan bikin ta amma ta dinga fadar haka yace " baki san an kusan bikin ta ba me zan yi da ita sanin kan kine da ina da sha'awar ƙara aure da tuni nayi amma ki bi ki dinga daga hankalin ki me kika nema wanda bana yi miki shi komai ina miki domin farin cikin ki amma bakya gani..kullum zancen ki kishiya,
Wannan littafin na kudi ne ki biya ni ki karanta halalin ki,
500 kacal idan ya zama document ya koma 1k

Amina alhasan Muhammad opay
8141785374
Ku turo da shedar biya ta wannan number 08141785374
Yan niger kuma 1000fcfah
ku turo ta my nita
Amina Muhammad alhasan 08141785374
sai ku turo min da shedar biya ta wannan number 08141785374
Free ya kusan karewa.
https://youtu.be/_IOc2pOwgKk
Copy is not allowed
Episode 9
Juraij idan fa kana so ni da kai mu zauna lafiya a cikin gidan nan to wallahi ka fitar da yarinyar

nan daga gidan nan abincin ma na hakura zan shiga kitchen da kai na , na dafa ana dole ne ni wallahi duk wani zance da zaka faɗamin wai an saka mata rana an kusan bikin ta an daura auren ne naga take taken ta ɗan haka tun kafin dare yayi mata tabar min gida na.
Yumna ce ta fito jin abin da take fadī ta yi murmushi iya labɓanta domin ta kara tun zura ahlam ai kuwa tayi faɗa ta shiga yi ta inda take shiga ba tanan take fita ba.
ɗurƙusawa tayi tace " aunty ina kwana..,
tayi pretending bama ta gane me take nufi ba da faɗan da take yi.
haushin ta ne ya kama ahlam ganin ta mai da ita yar iska cikin zafin rai tace " ke kwaso kayan ki , kibar gidan nan.,
da sauri yumna ta kalli juraij ganin ba abin da yace tashi tayi ta shiga daki daman itama ta gani haka kurum su dinga saka ta bauta sai kace wata jaka da sassafen nan shi gashi me mata yar gwal ta tashi ta yi musu breakfast itafa wannan abu gaba ya kai ta gobarar titi ajos.
kwaso kayan ta, tayi ta fito bata ko kalli inda suke ba ta fita taci sa'a gate din a buɗe yake fita tayi kai tsaye part din mommy ta nufa shima nan sun tashi suna breakfast ga mahaifin su juraij yana zaune shima sallama tayi ta sunkuyar da kai da sauri mommy ta ɗago tace " yumna ya kika dawo na ganki kuma da kayan ki Allah i saka lafiya me ya faru...?,
Alhaji Mahmud ya goge bakin sa da tissue ya tashi yace "  yusrah idan kin gama ki zo sai salisu ya ajiye a makarantar taku ya wuce dani motar da ake kai ki ta lalace..,
tsugunawa tayi tace " ina kwana..,
bata re da ya kalle ta ba yace lafiya qalau alhamdulilah kin zo lafiya ya su malam..
suna lafiya tace mai tare da tashi gaishe da mommy tayi batare da ta bata amsar tambayar da tayi mata ba Alhaji sallama yayi musu ya fita yusrah ta bi bayan sa zama tayi tace " mommy ta koro ni wai karna aure mata miji..,
dariya mommy tayi juhud kuwa daman tasan za'a rina an saci zanin mahauciya ci gaba da cin chips din'ta mommy tace " to shikkenan za mu haɗu dashi da yazama saunan namiji matar ka ta kori yar uwar ka kuma ka zauna kana yaƙe mata baki sosai mommy take faɗa juhud ko tari ba tai ba da ta gama sai ta rataya jakar ta tace " mommy sai na dawo...,
harara ta zabga mata tace " Allah ya tsare hanya..,
murmushi tayi tace " amin ya Allah ta fita.
gyara zama tayi tace " mommy ni bazan ƙara zuwa gidan sa ba tun da korata suke yi..,
bata dai ce mata komai ba sai daukar wayar ta da tayi ta lalubo number juraij bugu ɗaya ya dauka cikin bada umrani tace " kazo ina son ganin ka..,
bata tsaya amsa gaisuwar sa ba ta kashe wayar ta.
ɗaukan plate tayi tace " yumna kin ci abinci..?,
girgiza kai tayi tace " a'a banci ba.
zuba mata tayi ta tura mata gaban ta farfesun kaji ne ga buredi ci ta fara yi tana ci da biredi sosai duniyar yumna tai mata dad'i.
tashi mommy tayi ta hau sama
juraij ne yayi sallama yumna da take tsaka da cin kazar ta , bata amsa ba tsawa ya daka mata yace " ke bakya amsa sallama ne..?,
lashe hannun ta tayi ta saki wata uwar gyatsa ta kora da kunun tsamiya takaici ne ya ture zuciyar juraij ransa a matukar ɓace yace " ba magana nake miki ba ..,
da sauri ta juyo tace " uhmm ban jika ba ..,

kwafa yayi yace " ina mommy take ..,
nima ban san inda take ba da zata tashi bata sanar min ba.
da sauri ya ɗago jin amsar da ta bashi lallai yau idan be karya yarinyar nan ba to be ciki jinin Mahmud ba.
fisgota yayi ta faɗi ƙasa tare da sakin razananniyar ƙara saboda ball da yayi da ita ya mare ta sai da taga wasu taurari sun gilma mata a idanuwanta.
ba shiru mommy ta dinga hada matattakala biyu uku tana saukowa tace " juraij lafiyar ka kuwa me tayi maka banda ci mata mutunci da kuka yi kai da yar gwal shi ne yanzu ka biyota zaka karya ta ko to wallahi idan ka jamata wata nakasar wanda zai aure ta yace ya fasa kai zaka aure ta ko kana so ko baka so..,
da sauri ya ɗago jin furucinta na ƙarshe me zai yi da yarinyar nan , to ma ya sakata a wanne gurbin cikin kwantar da murya yace " mommy yarinyar nan bata da kunya wallahi dan baki ga maganar da ta faɗan ba tambayar ta nayi kina ina tace bata san inda kike ba lokacin da zaki tashi baki sanar da ita ba , ke sa'ar ki ce ko kuma ni sa'an tane take faɗan wannan maganar wallahi taci sa'a da banyi rugurugu da ƙashin ta ba dalilin kenan da ya saka ahlam tace baza ta iya zama da ita ba jiya cikin girma da arziki ta dauke ta , takai ta daki tace ga dakin ta to wallahi yarinyar nan ta daddaƙara mata bakar magana ahlam ta faɗa min ban goyi bayan ta ba ,
to nayi abokai sun zo suma tace ta zo ta dauko musu abinci ta kai musu nan ma sai da ta faɗa mata magana yau ma da safe sai da su kayi..,
jikin mommy yayi sanyi ta ɗaga yumna tace " kiyi hakuri jeki daki...,
tashi tayi tana ɗin gisa kafar'ta ,ta shiga dakin mommy zama mommy tayi tace " wallahi abin da ahlam tayi raina ya ɓaci wanne irin shashanci ne wannan yarinyar da an ma kusan bakinta kaima bita zai zai har ka bari yumna ta , tawo yawa wani shanyayye..,
shiru yayi ya zauna a ƙasa yace " kiyi hakuri mommy insha'Allah zan gyara kuskurena Alhaji ya fita ne..,
Eh wallahi be jima da fita ba tun da kuka dawo daga masallaci sai aka kira shi a waya bayan fitar ka za ayi meeting gaggawa shine fa ya fita da wuri shi zai sauke yusrah ma saboda motar da za'a kai ta , ta lalace...
Juraij yace " to Allah ya kiyaye hanya nima yanzu zan fita office..,
yauwa kama tuna min maganar auren yarinyar nan biki sai matsowa yake ya kamata kai a matsayin ka na babban wanta kuma ga ba ran mahaifiyar ta mu za mu zama komai nata mahaifinta ba karfi ne da shi ba bikin ya'ya har biyu kuma mata ba wasa ba ni ba zan iya tambayar mahaifinku ba idan ya ga dama yayi to falillahil hamdu amma dai kai , ka kawo abin da zaka kawo ai mata siyayyar kayan daki nima daga gurina zan mata na daki dana kitchen da kuma sutura...
Mommy ta fadi haka tana kallon juraij domin jin me zai ce .
Shiru yayi yana nazari Sannan yace " to zan turo miki kudin abinda ya dace sai kiyi mata Allah ya bada zaman lafiya bama lallai ayi bikin da mu ba zan tafi Ingila wannan project ɗin tare da ahlam...,
To Allah ya temaka amma da son samu ne ka zauna a yi komai da kai.
tashi yayi yana cewa ni zan tafi Allah ya tsaɓa mana abin da yafi zama alkairi.
Mommy tace " Allah ya kiyaye hanya.
to haka ranaku sukai ta zuwa suna wucewa kullum da abin da yumna za tai wa ahlam duk da

bata barin ta shigar mata guri amma sai ta san yadda akai ta takaleta sukai faɗa tun mommy bata lura har ta gane yumna matsokaniya ce hatta juhud da bata fiye zama a cikin gidan ba bata kyale ta ba mommy ta dage sai gyara mata jiki take yi tayi kyau gwanin sha'awa ga hutu da jin dad'i da take ciki.
Yau tun da safe take buga number na'ima amma shiru ba'a dauka karshe ma dai a ka kashe layin babban tashin hankalinta gobe zata tafi gashi batai abin da ta dace ba idan ta bar arlit bata san yaushe za ta dawo ba , bata kuma da kuɗin dawowa tun da suna komawa jarabawa za su zane ta gama secondary sai kuma auren su.
zaman dirshen tayi a ƙasa ta rasa me yake damun ta ko wayo za tai wa mommy ta , tafita ta nemo inda ake daukan mutane zuwa Saudiyya tana cikin wannan zance a zuciyar'ta taji sallamar juraij da abokinsa ahlam na take musu baya wannan abu na bawa yumna haushi dul inda juraij ya taka sai ta taka tamkar bata yadda dashi ba ta dinga leƙe mai dogon tsaki taja ta mai da hankalin'ta kan wayar ta tana amsa sallamar'su.
zama Muhsin yayi yace " my  friend...,
da sauri ta juyo gashe dashi tayi ta matsa daga gurin tayi nesa da su juraij yace " ina mommy take..?,
tun safe ta fita unguwa ta bashi amsa still hankalinta na kan wayar ta.
ji yayi tamkar yayi ball da ita Muhsin yace " yumna ba magana daga gaisuwa shikkenan nifa zuwa nayi muyu hira..,
ɗago da idanuwanta tayi ta kalli juraij da yayi kicin kicin da haɗe rai banda iskancin muhsin ya da faɗa mai an kusa bikin ta amma shine be jiba da yake kan albasa gare shi.
tashi tayi ta shiga kitchen tray ta dauki ta zuba mai snack da lemo ta kawo mai ta ajiye a kan center table.
godiya yayi mata ta mai da kan'ta ƙasa tace bakomai.
ahlam kuwa ji tayi tamkar ta har bata juhud ce ta sako farim ciki ne ya cika ta , ganin muhsin gaishe dashi tayi tana zama amsawa yayi cikin kulawa yace " ya aiki..?,
Alhamdulilah wallahi sai godiyar Ubangiji.
ta fada na kallon sa
Muhsin yace " ashe jamcy tayi aure..,
eh wallahi tayi aure ina ga wata biyu kenan da yin auren ta.
Kai ya gyaɗa yace " ta zubar da makaman boko kenan hakan na da kyau aure sittira ce ga diya mace ..,
dauke kai juhud tayi a zuciyar'ta tace kaga shege ko ina ruwan sa owo.
a fili kuma sai tace " haka ne wallahi shawarar da ya kamata ni da kai mu bawa kan mu kenan..,
dariya yayi yace " aini na samu juraij yana neman hana ni..
da sauri ta kalle sa cikin rashin fahimta tace " ya juraij ne ya hanaka yin auren..,
Muhsin yace " kusan haka ne wacce nake so yace an riga da an bada ita..,
kallon juraij tayi tace " yaya wace ita ...?,
juraij yace " shi da yake baki labarin ba sai ki bari ya karasa miki ba..,
kallon ahlam tayi da tai kicin kicin ta ɓata fuska tamkar ambata bishira da cewa ita yar wuta ce.
mai da kallon ta tayi gare sa tace " ya Muhsin fahimtar dani me yake faruwa..? wace ita yar gidan wace haka..?,
yumna da take zaune tana jin su sai tai kamar bata wajen juhud ƙara mai maita maganar tayi

Muhsin yace " yumna..,
Da sauri juhud tace " Qu'est-ce que tu dis...?,
Murmushi Muhsin yayi yace " juhud laifi na aikata ne..?,
kai ta girgiza juhud tayi tace " a'a amma ka kusan aikatawa saboda ba kyau nema cikin nema..,
Yumna tashi tayi daga gurin ta shiga daki da harara ahlam ta raka ta da ita.
Muhsin shiru yayi juraij yace " Muhsin yanzu mene amfanin abin da ka aikata...,
Muhsin yace " idan rabona ce Allah zai bani ita wallahi ina son yarinyar nutsuwar ta , ita ta ƙara jan hankalina gurin ta...,
da sauri juhud ta zaro ido sai kuma ta sheƙe da dariya har da riƙe ciki lallai ya Muhsin be san wace yumna ba wata ran sai ta saka shi hawan jini juhud tace " aunty ahlam bakya jin abin da yaya Muhsin yake faɗi.. ,

https://youtu.be/_lOc2pOwgKk
Copy is not allowed
Episode 10
Juhud naji mana bani da amsar bayar wa amma lokaci shi zai bashi amsa da kan'sa zai bambance tsakanin aya da tsakuwa.
kallon ahlam juraij yayi da sauri ta dauke kan'ta ganin irin kallon da ya jefe ta dashi Muhsin kallon juraij yayi yace " tun da ban same ta ba zan tafi idan ta dawo kuce ina gaishe ta.
tashi juraij yayi ya saka hannuwansa a aljihunsa yace " okay insha'Allah zata ji muje na raka ka ko..,
dafa kafadar sa yayi yace " no basai ka raka ni ba Nagode sosai...,
kai kurum juraij ya ɗaga ba tare da yace komai ba ,godiya su ahlam sukai mai ya tafi.tashi ahlam tayi tace " juhud sai da safe..,
ɗagowa judud tayi ta kalle ta tace " oh Allah ya tashe mu lafiya..,
a takaice tace amin ta fita a hanya suka ci karo da mommy suka gaisa mommy ta shigo zama tayi direba ya shigi da kayayyaki yusrah da ta sauko daga sama tace " mommy wanna siyayyar batai yawa ba ..? ke ba ganin inda za a kai ta kikai ba kike lodar wannan kayan..?,
judud tace " yauwa yusrah faɗa mata gaskiya mutumin da yake almajiri ina yaga inda zai zuba wannan kayan nan ni dan dai kar na fadi ne ace ni ban yi ba na hana ayi..,
murmushi mommy tayi tace " juhud kenan amma dai ko ba mu ga wajen ba hakkin mu ne mu siya mata ko..?,
hakane tace ta tashi tare da , daukan wayar ta , tabar gurin mommy kallon yusrah tayi tace " gobe fa dake zamu tafi...,
gyara zama mommy tayi ta miƙe kafar ta , tace " zama tayi akan kujera tace " dani kuma gaskiya ina da zuwa makaranta ki tafi da ya juraij..,
yana da uzuri nasan da zai kai ni, bana son tafiya ni kaɗai ne wallahi.,,
Ni da ace bani da zuwa makaranta dana raka ki wallahi amma gobe ina da test har biyu
Tashi mommy tayi tace " Allah ya temaka..,
Amin ya Allah tace da sauri yumna ta fito tace " mommy sannu da dawowa..?,
cikin sakin fuska mommy tace " yauwa ya kaɗaici..?,
murmushi tayi tace " alhamdulilah an daman mommy ina so naje gidan su kawata da suna Agadez suka dawo nan  yanzu mukai waya da ita tai min kwatance wallahi tun da nazu nake

neman number sai yau na samu ita ce wacce nake baki labari ban san ko ba zan ƙara dawowa ba nan kusa gwara naje mu gaisa..,
dan jim mommy tayi sannan tace " to ba damuwa bara na saka akai ki amma karki dade kinga dare na kawo kai abin da ya saka ma zan barki gobe zaki tafi..,
ran yumna be so ba da mommy tace kai ta za ayi to ta tafi ta zaga gari ko Allah zai saka ta ga masu daukan mutane tafiya makka amma bakomai za ta san yadda za tayi tace " to mommy ba damuwa bara na shirya..,
okay kiyi maza ki shirya bara na kirawo Salisu ya kai ki.
da gudu ta fita tana murna zama tayi a bakin gado rasa ina za tayi addu'a ta shiga yi a ranta tare da kiran layin na'ima cikin ikon Allah ta shiga ta ɗauka cikin zumuɗi tace " na'ima wannan wanne irin hulakanci ne ina ta kiran ki karshe ma sai kika kashe wayar wato wasa tare ci banban ko abin da kika samu shine bakya so na samu ko to wallahi bakomai kinyi da yar halak..,
hmmm wallahi aikine ya sha kai na amma ba damuwa bara na turo miki yanzu dan Allah idan na turo miki karki ƙara damuna da kira wallahi kina katsai min aiki na ..
saboda bakin ciki yumna kasa Magana tayi ta saki baki ta ma rasa abin da za tace .
jin alamar kudinta yana dab da ƙarewa sai ta kashe wayar ta ɗan jima a zaune sanan ra ji shiguwar messages da sauri ta dubu wani tsallam murna tayi kamar gurin ba nesa da inda suke da sauri ta fito tace " mommy ta turo min address din gidan ba nisa da nan gurin ashe ni kwatance da tai min ban gane ba Allah ya saka na kara kiranta na tabbatar basai ma ya kai ni ba dan gaba da kune kaɗan..,
Oh to Allah ya temake sai kin dawo komawa daki tayi cikin sauri take shiryawa har ta gama ta saka hijabinta sallama tayiwa mommy ta fito gate me gadi ya buɗe mata ta fita kallon ko ina take tun da ta zo yau ne ta fita unguwar shiru baka jin motsin komai sai na tsuntsaye da yake kusan rabin su ma'aikata ne a zaune a unguwar kuma manyan ma'aikatan gwamnati da na Company tafiya ta dinga yi tana dubu sakon da yake cikin wayar ta da yake har da sunan Company da yake daukar Mutane aikatau ta saka mata cikin sa'ta ta gano gurin anyi rubutu da manyan baki cikin harshen French an saka Fais semblant d'être humble (do garo da kai) da sauri ta tsaya tana tunanin to ta ina ce kofar shiga tana wannan tunani wani ya zo wucewa da sauri tace " bawan Allah ina wuni..?,
Tsayawa dattijon yayi yace" barka dai ya'ta..,
am Dan Allah tambaya nake..
dattijon nan yace " Allah ya saka na sani..,
yumna kallon gurin tayi ta nuna mai yace " dan Allah ta ina ake shiga gurin nan naga kamar katanga ce sai karamar kofa itama a kulle..?,
dan jim yayi yana karantar yanayin ta Sannan yace " eh ba nan ce kofar da ake shiga ba kofar tana can baya ina ɗaya daga cikin ma'aikatan gurin office wa kike nema...?,
ajiyar zuciya ta sauke ganin kayan ta ya tsinke a gindin kaba tace " daman ina so na tafi makka aikatau ne to ban san yadda ake abin ba wata kawata ce ta kwatanta min nan gurin...,
Oh masha Allahu ki godewa Allah ni ke da alhakin daukan duk wasu ma'aikata na turasu ƙasashe akwai agent din da zai raba su inda za su yi aiki acan amma muna da sharadi zaki saka hannu muje nayi miki bayani..
to ba damuwa muje zagayawa baya su kayi ta wata kofa suka shiga sai kalle kalle take ganin

ma'aikata suna ta sabgar gaban su wani office suka shiga ya zauna ya fito da wasu takardu yace " kin shirya nayi miki bayani..?,
yumna tace " eh na shirya..,
yauwa a ka idar tafiya aikin nan bana ɗaukan ƙasa da shekara Shata kwas sannan mun fi son bazzawara wacce tai aure tana da yara biyu haka amma yan matan ma muna ɗauka amma da saka hannu iyayen su sannan za mu kai ki muyi miki komai za kiyi shekara ɗaya kina biyan mu kafin ki fara cin gashin kanki kina.
kannata ne ya kulle tace " saboda me aka fi son bazaurawa...,
Masha Allah kina da kyan kai da kikai min wannan tambayar dalilina da yasa muka fi son daukan zaurawa saboda su, suna da yancin kan'su sannan duk abin da aka saka su za su yi, duk wani aiki na gida za su iya yin sa..
shiru tayi tana sauraron sa sannan tace " a gaskiya ni bani da aure amma sai bayan nayi aure na fito sannan zan yi wannan tafiyar saboda a gidan mu balallai a barni ba ,
okay ba matsala ko yaushe kika shirya zaki iya zuwa sannan akwai ka'idojin mu bama daukan mace mu kaita batare da anyi general check up ba sannan albashin ki na watanni goma sha biyu wato shekara ɗaya zamu riƙe shi saboda mun yi miki dawainiyar kaiki da kuɗaɗen mu , sannan wannan company na zata dena iko da ke ba sai bayan shekara ɗaya dole kibi dokokin mu idan mace taga ba zata iya zama ba tana bukatar canjin waje ko dawowa to fa sai ya biya mu tas abin da muka kashe har da ribar dubu dari bakwai....
da sauri ta ɗago jin abin da yace na ƙarshe murmushi yayi yace " naga kin kalle ni maganar tayi miki nauyi ne akai..?,
yumna tace " kusan haka ne ,
cure hannuwansa yayi guri ɗaya ya sarke su yace " wannan company yana kashe makudan kuɗaɗen gurin tafiyar yan aikatau dole zai mai da kudin sa har da riba..,
ajiyar zuciya ta sauke tace " hakane amma kawata batai min wannan jawabin ba ...,
wace ya sunan ta a wacce shekara ta tafi..?
ya jero mata wa'yannan tambayoyin
yumna tace " sunan ta Na'ima hamidu Poussin yar Agadez ce shekarar ta ɗaya bana jin ma ta cika ɗaya amma kuma ta turo da kudade a gyara musu gida ya akai ta samu kudi bayan kune da kudin ta bata gama biyan ku ba..,
Murmushi yayi yace " oh na gane ta sosai ana samin alkairi a cikin tafiyar idan har mutum yayi amfani da damar sa sai ya tara abin duniya bayan ya gama ko kuma yaga ya gaji da zaman sai ya dena ya dawo gida ya ci gaba da harkokin sa da facaka da kudin sa son ran sa akwai matan da suka zama hajjiyoyi ko bayan sun dawo to ƙaramin mutum ma be isa ya kalle su ba suna da yancin kan'su sun san me ne yancin su, su suke zama matan mayan shuwagabanni da manyan yan kasuwa kinga kamar ke yadda kike da wannan kyan ina me tabbatar miki idan kika je zaki samu alkairai masu tarin yawa mayan kuɗaɗe sai dai kiyi kyautar su badai a baki ba...,
kallon agogon wayar ta tayi tace " hakane Nagode sosai lokaci yana ja gashi saka min number ka idan na tashi zan kiraka..,
karba yayi ya saka mata , sannan yace " tsaya a dan kawo miki abin jiƙa maƙoshi muna ta koro bayani na barki ba wani dan abu..,
murmushi tayi tace " a'a wallahi Nagode sosai Allah ya saka da alheri..,
amin ya Allah yace tai mai sallama ta fito tafiya ta fara tana ta tunane tunane kala kala har ta

kusan zuwa gida ta rasa gano bakin zaren to ita da take so tayi shekara ɗaya ta dawo mene amfanin zuwa aikin nan shekara ɗaya fa za tayi tana kwaɗago amma cikar burinta da mafarkin rayuwar ta fa shikkenan sai tayi shekara biyu lokacin ta tara abin da take iya ganin zai fiddasu daga cikin talaucin da suke ciki ,
har ta ƙarasa bata dena wannan tunanin ba tana shiga aka tada sallar magariba juraij ne ya fito yana sassarfa da alama masallaci zai je matsa mai tayi tana kai da kan'ta shima da yake yana da uzurin gaban sa be kulata ba ita tun da ya kusan targaɗa'ta ta dena shiga sabgar sa ba ruwanta dashi tunda mugu ne.
bata tarar da kowa ba acikin parlour dakin da aka sauke ta nan ta shiga ta dauro alwala ta tada salla bayan ta idar ta, tashi ta  fito bedroom din mommy ta shiga sallama tayi tana zaune tana jan carbi durkusawa tayi tace " mommy na dawo...,
Murmushi tayi ta ajiye carbin hannunta tace " to ya suke da fatan suna Lafiya qalau..?,
murmushi yumna ta mai da mata tace " alhamdulilah suna lafiya tama ce a gaishe ki da ba dan tafiya zan yi ba ta , tazo kun gaisa..,
Allah sarki ba damuwa wata ran ta zuwa idan kin zo garin.
tashi tayi tace " nima haka nace mata ..,
fita tayi ta zauna akan kujera tana game da wayar ta a yanzu da ta kawo karshen wannan matsalar tata sai take jin bata da wata sauran damuwa malam da sauri zuciyar ta , ta buga tasan ba lallai ya amince da tafiyar ta ba , amma zata yi duk yadda za tayi ya amince idan kuwa yaƙi to za tai mai layar zana sai dai ya shafa yaga babu ita haka kurum su kenan ba wani me jin dad'i kowa wanda zai aura faƙiri ne haka ma wai gwara ita da zata auri mamman saurayin shamsiyya keke ne dashi yana yawo yana siyar da su  karas da ɗa'ta..
dan haka wallahi ba zata kashe kan'ta ba haka kurum sai kace an yiwa malam kauri da kan kifi ya kasa fahimtar idan burin ta da mafarkin ta ya tafi..
ke da sauri ta ɗago ganin juraij sai ta kau dakan ta tace " na'am..,
tashi kije ki share min daki na dana ahlam..,
da sauri ta kalle sa tace " tafa ce idan ta ƙara gani na a cikin gidan ta sai ta yanka ni..,
ni nace miki, ki tashi kije kiyi aikin da na saka ki.
tashi tayi bata ce komai ba ta fita tana shiga pary din ta , samun ta , tayi tayi ɗare dare tana kallo Oni jikar mutum goma kowa da irin tashi salon kaddarar ita kuma wannan tata ta kallo ce kuma lalurar kallon a waya take yin ta ..,
ta faɗi haka tana shiga cikin dakin ahlam juyowa tayi tace " baki iya sallama bane ko ce miki akai nan chochi ce..?,
ɗaga kan'ta sama tayi tana karewa dakin kallo tace " ikon Allah sai nake ganin kamar na shigo chochi jin wasu maganganu na tashi tamkar na arnan da suka dade ba su san waye Allah ba , bisa dukkan alamu ma sallar da aka yi ta magariba ba lallai sun yi ta ba..,
Da sauri ahlam ta tashi tace
"Are you even in your right mind? Do you know what you're saying to me..?,,
murguɗa mata baki tayi tace " aikin san bana jin turanci da kiyi min da yaran da zan gane na baki amsa dai-dai da abin da kika faɗa min..,
fasa marin ta tayi taja kwafa ta dauki wayar ta , tabar gurin tsaki taja ta fara gyare gyaren gidan ranta duk a ɓaci ta rasa ahlam wacce irin mace ce wannan ƙazanta haka kullum sai dai ta bulluwa jikinta turare taci kwalliya tamkar zata je gasar sarauniyar kyau amma daki ba kyan

gani. gama gyara parlour tayi ta tafi bedroom nan ma kaya ne sunfi set ashirin a ajiye a gefen gado ga Landry basket amma ba amfani kwashewa tayi ta gyara ko ina tare da sala Room freshener sai karfe takwas sannan ta gama komai ta fito ko arzikin kallo bata samu ba daga gurin ahlam balle a kai ga godiya a gaje ta koma tana shiga tayi sallah bayan ta idar ta fito kan dining table ta nufa ta zuba abinci ta fara ciki bayan ta gama tayi wanka ta kwanta.
tun asuba tayi wanka ta shirya wani irin zumuɗi take tun da ta kashe wannan wutar gwara taje can itama ta ayi wacce za ayi,
karayawa tayi direba ya kwashi kayayyakin ta ya saka aboot sanan ta shiga Alhaji ya bata kuɗi godiya tayi mai suka dauke hanyar Agadez lokacin da suka isa karfe goma da rabi fitowa tayi malam da yake zaune yana biyawa almajirai karatu ta ɗago ya kalli Hajiya mommy yace " sannun ku da zuwa..,
durkusawa tayi tace " yauwa malam mun same ku lafiya..?,
Malam yace " lafiya qalau alhamdulilah ya kuma ya yaran namu da me gidan naki..?,
murmushi tayi tace " alhamdulilah suna lafiya qalau..,
masha Allahu Allah ya kara shiryar mana da su kan tafarki madaidaici ina juraij yake yau ban dashi kuka zo
Mommy tace " amin ya Allah baya nan yana gurin aiki..,
to Allah ya temaka Allah ya bada abin da ake nema..
tashi tayi tana amin ya Allah.
Malam barka da safiya.
Barka dai yumna kin dawo lafiya.
lafiya qalau alhamdulilah.
shiga cikin gidan mommy su kayi su baba lami suka tarar suna zaune suna hira gaisawa suka yi sannan suka kawo musu abin kari kunun tsamiya ne da ƙotsai, mommy tace " alhamdulilah wallahi na koshi..,
Inna hadiza tace " a'a kodai irin namu ne ba zaki ciba abin da kunyi tafiyar mota duk abincin ya zazzage..,
a haba yau na sana zuwa gidan nan wallahi na koshi
Cewar mommy.
to ba damuwa yumna ba magana kin ja gefe kinyi shiru,
da sauri yumna ta kalle su tace " nafa gaisheku...,
Baba lami tace " haka ne wallahi..,
Kaya aka shiga shigo dashi su baba lami wannan ta kalli wannan wannan ta kalli wannan ganin kamar za'a buɗe shagon sai da kayan kitchen da na daki..,
shugowa malam yayi, yayi mata godiya haka ma su baba lami inna Hadiza tace " to yumna ki dubu irin kokarin da wannan baiwar Allah tayi ki daure ko me zai faru kiyi koyi da halin manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama kiyi hakuri shi zaman aure ibadane yi nayi bari na bari shikkenan ko dan martabar mahaifinki da gidan da kika taso karki kalli na waje su baki sha'awa kowa fata yake ya sami irin ni'imar da kika samu kalli kaya kamar yar gidan wani attajirin me kudi dan girman Allah kiyi hankali ki nutsu..,
ƙasa tayi da kan'ta ta ta share kwallar karya tace " insha'Allahu zan yi iya bakin kokarina da yardar Allah ba za kuji wata matsala daga gurina ba..,
Dad'i ya kama malam ganin yadda suka haɗu sukai mata faɗa kuma taji ta amsa albarka ya

saka mata ya koma zaure domin ci gaba da karantu
Karfe biyu mommy ta tafi tare da bata kudi sosai tayi murna.
karfe takwas na dare mamman ya aiko kiran ta ,
sai da ta gama ɓata lokaci sannan ta fita tana wura hanci tsayawa tayi a kofar gida ta jingina da kofar gidan su tace " barka da dare..?,
Barka dai masoyiya kinga kuwa yadda kika koma tamkar wata balarabiya ke daman matar manyan ce irina...
da sauri ta ɗago jin furu cinsa na ƙarshe tace " Mamman kai sauri ka fadɗi abin da ya kawo ka saboda bacci nake gobe zamu fara zana jarabawa..,
murmushi yayi yace" wallahi na ƙagu ku gama jarabawar nan na ganki a cikin gidana kin zama mallaki na yumna ranar ba ƙaramin dadi zan ji ba wallahi yau ga yumna ta zama mallaki na muna tare da juna kai Allah ya nuna min ranar nan yasin ranar sai nayi sadakar nama asan cewa yau dan gidan sarkin fawa zai auri yumna zubin larabawa matar manya...,
kallon sa tayi yaci hular kauraye dan tsan hannun sa da guro da yake rigar jikin sa yar shara ce...
dauke kai tayi ita bata san wacce irin kaddara ce ta kai ta ga soyayya da mamman ba gaba ƙi ɗaya alamun rashin wadata ta game ko ina na jikin sa rigar duk ta kode dan hala wutsiyar ragumi tayi nesa da ƙasa dole ta nuna mai banbancin tsakanin ita dashi ta rabe mai tsakanin a ya da tsakuwa...

Copy is not allowed
Domin jin audio din Yan zaman Makkah Ku danna wannan link din sannan kuyi subscribe Dan Allah.
https://youtu.be/cDE5bjYY2HY

---

https://www.arewabooks.com/chapter?id=6817816be532b4a92550458c
Episode 11
Masoyiya ya kikai shiru kin barni ina ta zuba yawa ya'yan kaɗan ya..
dafa kan'ta tayi tace mamman ciwon kai nake ina buƙatar hutu kazo ka ci kani da zance kaga sai an jima.
sakar baki yayi yana kallon ta har ta shiga cikin gidan su shafa kan'sa yayi yace " bakomai aski idan ya zo gaban goshi yafi zafi..,
kai tsaye gidan su ya nufa tun daga soro yake jin tashin muryar mahaifiyar sa da sauri ya ƙarasa tare da yin sallama mahaifinsa ne ya amsa amma ita ko kallon inda yake ba tai ba ta ci gaba da cewa Wallahi idan har kina son zaman lafiya karku kawo min wannan mara kunyar yarinyar cikin gidan nan kaf garin nan waye ban san ta ba a fagen rashin kunya yau kusan sati uku kenan ta ganni a hanya ko nunawa ba tai ba , ta sanni balle ta gaisheni dan haka kuka sake ta shigi cikin gidan nan sai ta dandani ƙudar ta sai na gasa mata aya a hannu me ake yi da mara tarbiyya ya kwalla fa rai sai ya aure ta , duk yabi ya rame ya kan jame ni wallahi da ace yar uwar ta ce nazeefa bazan ce bana so ba daman ko lokacin da kakai kuɗi badan raina ya so ba , bana son ta bana son wannan auren ba da yahuna za ka yi shi ba..
Yan zu asabe abin da ki kayi in kyau ta kenan me yarinyar nan tayi miki duk kin bi kin tsane ta ita ba aikata wani abin take ba na ba dai-dai ba amma lokaci ɗaya kin tsane ta haba asabe abin

da ki ke aikatawa be dai-dai ba yanzu an kusan biki shine kike tada mana da hankali da me yaron nan zai ji da kunji kunjin biki ko da abin da kike yi..
cewar baffa mahaifin Mamman
Mamman wuce wa yayi bece komai ba zama yayi a daki ya zabga tagumi inna tayi yumna tayi dame zai ji,
Kwance yayi ya rasa in inda zai saka kan'sa saboda tashin hankali yana son yumna baya son abin da zai raba shi da ita ,
yana so su gina ingantacciyar rayuwa me tsafta wacce zata ginu har zuwa tsufansu share zufa yayi lokaci ɗaya zazzaɓi ya rufe shi gyara kwanciyar sa yayi ya kudindine a bargon sa da ya gaji da cin duniya duk ya farfarke.
daga haka bacci ya dauke shi
Washegari yumna suka fara jarabawa tun da suka fara bata ƙara saka Mamman a idonta ba duk kiran da zai mata bata ɗaukar wayar ace warta zai takura mata rayuwa har suka gama.
washe garin da suka gama aka kawo kayan lefen su ranar inna Hadiza har rawa tayi domin saurayin shamsiyya yayi bajinta ya zuma mata kaya, Mamman kuwa ba wani abin arziki ashe abin azuciya yake bawai karfi bane haka. Baba lami tace suna zaune suna cin abinci yumna ko bi takanasu ba tai ba to ita me ne haɗin ta da wannan kaya ko a zuciyar ta bata ji rashin dad'i ba, saboda sai kana son mutum kake kishin sa.
Shamsiyya ce ta kallo yumna ta gefen ido ita fa wannan kwantan ɓaunar da tayi bata gane mai ba anya kuwa ba akwai wata a ƙasa ba duk son duniya irin na yumna ta nuna ko a jikin ta ko dai wani abin arzikin Mamman yake tsara mata shi ya saka mata sauke mai buhun tujara akan sa ba.
Assalamu alaikum
baba lami tace " wa'alaikis'salam...,
yaron da aka turo yace " wai yumna tazo inji Mamman..,
kallon ta baba lami tayi taji me za tace, ita kuwa yumna bama ta nuna ba taga yaron balle a saka ran za tayi magana wannan yarinya ba dai kafiya da taurin kai ba yawa kafurar farko haka baba lami ta ce a zuciyar'ta afili kuwa sai tace " yumna ke fa ake kira..?,
ajiye wayar ta tayi akan cinyar ta , tace " baba ai ke zaki bashi amsa bani ba , yanzu ina magana ina saka kafana ina fita hmm labari zai sha bamban zaki kwashe min albarka ne kuce bani da kunya...,
inna Hadiza tace " ta Allah ya kyauta kai jeka kace tana zuwa..,
tashi yumna tayi ta saka hijabinta ba wanda ta yiwa magana ta fara tafiya da sauri baba lami tace " yumna ba zaki dauki daduma ba kullum baki da tunanin karrama bako ki saka mai abin da zai zauna sai ki bar shi a tsaye sai kace wani soja..,
Jingina tayi da bango jikin ta duk yayi sanyi zuwa sati me zuwa tasan i yanzu tana gidan Mamman dan haka jikin'ta yayi wani irin sanyi amma zuciyar nan a tsaye take tana nan akan kudurinta tace " nazeefa jeki, ki dauko  min..,
tashi nazeefa tayi cikin sauri karta dake ta , ta miko mata amsa tayi ta fita yana zaune akan wani dutsai shifiɗa dadumar tayi ta zauna tace " gani...,
da sauri ya ɗago ajiyar zuciya ya sauke yace " wallahi ban ma san kin iso ba , ina ta tunani na zata ba zaki fito ba wai masoyiya me ya canza min ke lokaci guda na kasa gane kan ki bakya daukar waya ta ko zanyi kira ɗari ba zaki dauka ba dan girman Allah yumna ki tausayawa

zuciya'ta dame zanji ke kiyi innar mu tayi   wallahi ina cikin matsala..,
kura mai ido tayi ta kasa kiftawa azuciya ta tace kai taga me sauƙi ce ƙasa yayi da kan'sa ya ci gaba da cewa ki tausaya min, ko yaya ta gurin ki na samu rangwami.
ajiyar zuciya ta sauke ta dauke kan'ta daga kallon sa da take tace " Mamman auren mu ina tunanin ba me dorewa bane tun yanzu ka fara korafi jarabawa nake ina son hutu amma kai baka fahimtar haka ko wanne bawa akwai irin tashi ƙaddarar ka dinfa saukaka kanka Ubangiji shi ne masanin gaibu..
da sauri ya ɗago yace " to shikkenan wallahi yumna ko me kika yi daidai ne agurina bakya taba yin laifi zan jure komai nasan wata ran sai labari..,
anya kuwa Mamman ba jinsin mayu bane kai akwai lauje cikin naɗi irin wannan naci haka turkashi ta raya wannan a cikin zuciyar ta , afili kuwa sai tace " dare yana yi..,
da sauri sauri yace " to dame dame kika tsara ina so naki kudin da zaki yi duk abin da kike so inhar be fi karfina ba ..,
tashi tsaye tayi ta ninke dadumar ta , tace " ah barshi wallahi kayi wani abin da bakai ba , bani da bukatar komai ba abin da na tsara, ba abin da zanyi..,
saboda me ranar fa farin ciki ce..?
limshe idanuwan'ta tayi ta saki sani murmushi wanda ake kira da yafi kuka ciwo tace " Mamman kenan ni nace kayi abin da ya dace..,
tashi tsaye yayi yana karkadai rigarsa yace " karfa ya zamo abin Magana yumna ace ba kiyi komai ba..,
au kenan dan riya zaka bani kudin, da ba dan haka ba ko karfanfana dattin aljihu ba zan gani ba ta faɗa tana tsare shi da manyan idanuwanta.
ajiyar zuciya ya sauke yace " wallahi Allah ko ɗaya kawai dai kinsan halin mutane musamman ma kawayen ki da suke yan duniya kar su dinga ganin kamar bakiyi sa'ar miji ba , bana so a dinga yi miki kallon kaskanci yumna idan ina da hali duniyar nan gaba ki ɗaya ace mallakina ce zan iya mallaka miki..,
kallon sa take baki sake tace " gwara da ka fito fili ka faɗa min abin da ke cikin ranka ka dena boyewa a zuciyar ka, kaga kawaye na ne ni da su kallon da kake mana kenan to ba komai bakomai Mamman akwai can za ayi hisabi wato shi ya saka yan gidan ku suke min wani irin kallo dana kasa fassara shi...,
Haba yumna wai me ya saka duk hanyar da na kauce kar na biye miki sai ki ƙara fasa wata ni da baki na , na faɗa miki haka  yumna ki dena abin da kike yi kar hakkina ya kama ki..
banza tayi mai ta shiga cikin gida tana kun kuni.
Baba lami tace " yumna lafiya kika shigo kamar an jewoki...?,
saita kan'ta tayi domin kar su gane me yake faruwa tace " tofa na shiga uku gani kika yi an cillo ni..?,
kallon kallo suka shiga tsakanin inna Hadiza da baba lami ganin haka yumna ta shiga daki tana dariya tunawa da tayi ta bar wayar ta a tsakar gida da sauri ta fito ɗaukan ta tayi ta shiga dakin su zama tayi ta zuba ta gumi shamsiyya ce ta shigo zama tayi tace " yauwa yumna me kika shirya lokaci fa yana kurewa ga katin can ma da Mamman ya bani jiya baki taɓa , ba ni nawa har na gama rabarwa kamar wacce bakya son auren nan yumna me yake faruwa..?,
afusa ce tace " uwar ki ce daman tun ɗazu naga bakin ki yana motsi ashe abin da zaki tambaye ni to ban sani ba idan ma wani ya turo ki kije ki faɗa mai duk abin kikai niya yau nake jin bakar

jaraba ina cewa ni nakawo Mamman gidan nan ina son sa ....? sai kuma na dawo nace bana son sa saboda bani da hankali ban san me yake damuna ba to wallahi duk wanda ya ƙara tarata da wannan maganar nan sai na gurje mai baki, haba daman tun da na dawo kallon da ake min kenan to yasin zan wasa wuƙa ta wani ya kara tarata da wannan zancen zai ga me zai faru tun da ku baku san zuru ba..,
sum sum shamsiyya ta tashi ta fita baba lami ta fito tace " wai ke yumna me ya saka kin iya neman magana da tujara yanzu da ace tayi abin nan bata neme ki fa Allah ne yasan kadai me zaki yi mata wallahi ki gyara halayen ki gidan wani zaki duk wani datti ki zubar dashi a kofar gidan nan idan kika tafi dashi wallahi ba lallai su raga miki ba , kamar yadda mu muke raga miki ba...,
baba lami muna ganin mutuncin ki tun kafin ranki ya ɓaci ki ɓace mana daga gani ko yanzu mu tarwatsa miki ƙwaƙwalwa..
da gudu baba lami ta fita har tana tun tuɓe yumna tana ganin ta fira, ta kwanta tana dariya har da riƙe ciki ta sani sarai idan ba haka tayi mata ba , ba zata rabu da ita ba zatai ta Magana ne ita bata san zuru ba , har sai malam ya shigo ya iske ta , daman ta lura haka take so ɗaga ƙafafuwan'ta sama tayi tace "maganin biri ɗan katan uwa wace miki barno gabas ce wallahi kafin na bar gidan nan sai na saita muku zaman ku yan durin uwa haka kurum ku takura min da wani banzan zance aita magana ɗaya aure ne , na yarda zanyi to me kuma kuke bukata bayan wannan..,
Bayan fitar baba lami dakin inna Hadiza ta tafi ta zauna tana zare ido sai leke take yawa wacce tayiwa sarki karya ganin haka inna Hadiza tace " lami lafiya naga kina ta gumi..?,
hmmm yaya yau ni naga tashin hankali daman ni nasan yarinyar nan wallahi ba ita kaɗai bace shi yasaka take iya shegen da ta ga dama malam be sani ba tsoro na ɗaya na fadawa malam abu ga ɓaci..
Kama haɓa inna Hadiza tayi tace " me tace miki an shiga uku..?,
hmmm ce min tayi zata fasa min ƙwaƙwalwa idan ban fita daga sabgar su ba ta faɗa ƙasa ƙasa domin tana gudu ta jiyo su lamari ya ɓaci..
wani yawu ya haɗiye me ɗaci tace " mun shiga uku ni wallahi dama yau zata bar gidan nan , taje zan ta ƙarata sai barazana take mana da rayuwar mu daga wancan sai wannan kalli fa abin da tayi mana ƙwanaki Allah ne yayi da sauran kwanan mu a gaba..,
Dari biyar ne ba yawa ki biyani hakkin rubutuna karki bari a sato ki karanta...
8141785374
amina Alhasan Muhammad opay
Yan niger
My nita
1000fcfah
Ku turo sheda ta wannan number
08141785374
Dan Allah idan baki shirya ba kar kiyi min magana.

Copy is not allowed
Domin jin audio din Yan zaman Makkah Ku danna wannan link din sannan kuyi subscribe Dan

Allah.
https://youtu.be/cDE5bjYY2HY
____________________
https://www.arewabooks.com/chapter?id=6817816be532b4a92550458c
Episode 12
Baba lami tace " wallahi kuwa gwara tatattara ta bar gidan nan ko masa mu sukuni haba wannan masifa haka dame tayi kama..,
har karfe tara suna tattaunawa akan wannan matsala ta yumna washegari shamsiyya ta fita tana rabon katim yumna tun da ta fita yumna take Allah Allah ya dawo ta, taci uban'ta tun da ta faɗa mata bata ji ba to za tayi maganin ta.
tamkar wacce tayiwa sarki karya haka ta ɗinga za gaye tana kaiwa tana komowa su inna Hadiza ido ne kawai nasu.
domin lamarin yumna sai addu'a har wajen azahar tana wannan kaiwa tana komowa domin yau dole ta hukunta shamsiyya dan uwar baban ta.
Assalamu alaikum da sauri ta fito jin sallamar shamsiyya sai dai wani abu da be mata dadi ba tare suke da malam dole tayi saranda ja da baya tayi malam yace " yumna ashe baki da lafiya yanzu yar uwarki ke faɗa min me , me ya saka tun da wuri baki faɗamin ba.?,
ƙasa tayi da kan'ta tace " naji sauki ma bakamar lokacin da na tashi ba..,
zama yayu cikin kulawa yace " meke damin ki..?,
yumna tace " zazzaɓi da ciwon kai ne amma alhamdulilah yanzu naji sauki.,
to Allah ya ƙara sauki,
amin ya Allah tace.
tashi yayi yace " shamsiyya jeki ki dauko min allo nayi mata rubutu..,
shamsiyya da , daman tana tsaye tun da ta shigo ta kalli yumna tasan yan bala'in sun motsa.
shiga dakin sa tayi ta dauko mai allo yumna ta shinfiɗa mai tabarma zama tayi a kusa da shi rubutu ya zauna yana yi jefi jefi yana tambayar ta ko tana da , damuwa.
yana tausayin rayuwar ta sosai saboda bata da uwa shiɗin ba mazauni bane balle ya san me yake faruwa duk da yasan halin yar tasa ba kanwar lasa bace.
yumna bata nuna mai akwai wata matsala ba da ya gama ya wanke ya bata , tasha amsa tayi tasha suka ɗan yaɓa hira ana kiran sallar magariba ya fita ita kuma, ta tashi tayi sallah,
bayan ta idar ta kwanta a tsakar gida tana jij Radio da wayar ta zama kusa da ita shamsiyya tayi sarai ta ganta sai tai kamar bata ganta ba ta ci gaba da jin radio ta idon ta a rufe yaran gidan suka ta wasan jakai kwarai yumna tayi lafiya da , dane tun da ta fito tsakar gidan nan , ba wanda zai ƙara wani kwakkwaran motsi idan kuma mutum yayi taurin kai tofa jikin'sa zai faɗa mai.
tana cikin jin radio shazali dan gidan baba lami ya faɗi mata aikuwa yaci ubansa domin duka tayi mai tas tare da han kaɗa shi, taja tsaki ta koma saki ta kwanta.
baba lami tana jin ta amma batayi ƙoƙarin magana ba domin ba mutunci za tayi mata ba.
washegari shamsiyya ta dinka musu kayan su da yake ta iya ɗinki yumna ce dai bata iya ba saboda ita bata ga me za tayi da sana'ar basir ba.
bayan ta gama ta kai mata wajen kayanta ta ajiye.
haka rayuwa taci gaba da wakana yau ana sauran kwana ɗaya daurin auren su kowa ya zo na arlit amma ban da ahlam da juraij hakan be wani bawa yumna mamaki ba tun da tasan shi dai

ba mutunci ya cika ba ,
shi da matar sa biyu ce ta haɗu shi ba mutunci haka ma ita, juhud ma bata zo ba sai yusrah sai mommy da kakarta tawajen uwa sosai suka nuna mata gata domin ko dinki ɗaya bata saka ba akayan da Mamman ya kawo mata.
zazzabi ne ya rufe ta fa'iza da nana suna tare da ita fa'iza ce tace " wallahi yumna banga bin damuwa ba duk kinbi kin takura kanki ke wallahi ki godewa Allah ma zakije kici yancin kanki..,
murmushin tayi, ta gyara kwanciyar ta zuciyar ta ba dad'i in banda tsabar rashin hankali wanne cin yan cin kai ce mata aka yi anan gidan, ba tacin yan cin kan'ta.
ita wannan ciwon bawai na damuwa bane tana ganin bakwan watan ta dab yake da zuwa cikin ta ma ciwo yake , tashu tayi ta dafe kan'ta tace " dan Allah cewa mommy bani da lafiya kaina ciwo yake da ciki na..,
tashi fa'iza tayi ta fita ba jimawa gabaki ɗayan su , suka zo har da yusrah.
mommy tace "subbanallahi tun yaushe ne baki ɗa lafiya amma kikai shiru da bakin ki...?,"
amai ne ya taso mata da sauri ta fito tsakar gida ta dinga kwara shi kowa sannu ya dinga yi mata bayan ta gama mommy ta wanke mata jiki kamata tayi suka shiga daki ta kwantar da kan'ta a cinyar kakarta tana sauke a jiyar zuciya daman haka period ke mata , bata mata , ta dad'i baka ramar wahala take sha ba.
magani mommy ta bata , tasha bacci ya dauke ta kamu ba , ba ai yi da ita ba saboda ba lafiya sosai take jin jiki,
washegari

RANA bata karya sai dai uwar ɗiya taji kunya.
sosai mutane suka taru daga gari daban daban domin malam na mutane ne ga kuma mahaifin Mamman alhaji Dauda me wuƙa sarkin fawa, masallaci ma kasa daukan mutanan yayi wasu suna waje daurin auren shamsiyya aka fara sannan na yumna lokacin da me shela ya sheɗa an daura auren ta ba ƙaramin tashin hankali ta shiga ba , tuni ta fara kwara a mai jikin ta ya zugage tas mommy ce ta gyara ta tare da bata magani bayan an gama MAMMAN da saurayin shamsiyya suka shigo domin gaisuwar surukai sai a lokacin ma ya ga bata da lafiya sosai ya tausaya mata .
bayan ya fita ya koma gida mahaifiyar sa sai cika take tana batsaiwa.
ko gaisuwar'sa bata amsa ba.
wannan kenan
da misalin karfe biyun suka tafi sukai mata jere dole sai da aka dawo da kaya da yawa saboda daki daya ne da ban daki sai kitchen shima ba wani babba ba yusrah tace " kinga ko abin da nake faɗa miki yanzu ya za kiyi da wannan kaya..?,
Mommy tace "'siyarwa zanyi na bata kudin sa mata wani amfanin taja jari..,"
shiru yusrah tayi bata ce komai ba Hajiya anni kakar mahaifiyar ta , tace " aikuwa kin kyauta Allah yayi albarka...,
amin tace da misalin karfe Biyar Na Yamma mommy ta shirya yumna cikin wani lece pink colour ba ƙaramin kyau yayi mata ba duk da saboda da cutar da tayi ta zabge ta rame lokaci ɗaya.
nasiha tayi mata kuka kawai take yi share hawaye bayan ta gama yi mata faɗa ta haɗa su, su da shamsiyya ta kara yi musu sannan malam da su inna bayan sun gama daman masu daukan amarya suna jiran su yumna da ta fito sai da ta juyo ta kara kallon gidan su hawaye ne suka

ƙara zubo mata , da kafar dama mommy tace ta shiga cikin motar.
shiga tayi ta kifa kanta ta ci gaba da kuka.

har suka isa nan ma da kafar dama mommy tace ta shiga batai musu ba ta shiga da ita kai tsaye gurin mahaifyat sa , suka nufa sallama su kayi kanwar sa hindatu ce ta amsa amma innar su Mamman ko nunawa ba tayi ba tasan da tsayuwar su.
shigowa su kayi wasu suka tsaya a waje mommy tace " barka da yamma ya taro..?,
dakyar tace " barka dai alhamdulilah..,
sosai mommy take mamaki to ya akai bata san da wannan matsalar ba , da baza ta bari ayi auren nan ba , kar ta takurawa yumna danne abin tayi tace " masha Allah to ga amana nan mun kawo miki duk..
ai bata karasa ba tace " da kata ban amshi wannan amanar ba dan haka ku tattara ƙafafuwan'ku ku fitar min daga daki kafin ba gurza muku tashin mutunci.
tashi su mayi yumna tamkar zata fadi saboda tashin hankali daman fa'iza ta dade tana faɗa mata innar su hindatu bata da kirki sai yau ita tashe da , da maganar fa'iza a gaban jama'a ta tozarta ta lallai jiya ba yau ba , ban da tayi sanyi yasin sai dai ta saka danta ya sake ta daman haka take bukata.
dakin ta suka kaita sosai mommy take cikin ɓacin rai faɗa ta kara yi mata tai mata sallama su fa'iza ma ba jimawa suka tafi.
zazzabi ne ya kara rufe ta da gudu ta fito tana kwara amai tamkar zata amayar da ya'yan hanjin ta innar su hindatu fitowa tayi ta kama kugu tace " wallahi ba zata sabo ba daman da ciki kika shigo min cikin gidan ɗana..,

ba karamin daga mata hankali wannan maganar tayi ba da sauri ta ɗago lokacin Mamman ya shugo yana baza babbar riga jin abin da mahaifiyar sa tace da sauri ya ƙara so cikin ɗaga murya da faɗa tace " gata nan ta shigo maka da ciki cikin gidan ka dan haka wallahi sai ka saketa ba zan yarda ba ta zauna min da cikin shege a cikin gidan nan ji yadda ta ɗashe tayi fari anzo za'a cuci ɗana ayi laulayi a gidan sa dan kirufawa kanki asiri kawayen ki ba ƙananan karuwai bane dan haka kaji na rantsai maka idan baka saketa ba sai na tsine maka kuma saki uku nake so kayi mata domin wa'yannan mayu ne tsaf ubanta zai ƙara rubuce ka akan sai ka sake ta ga yarinyar nan yar mutunci na kawo maka amma kaki ka aura ka ɓuge da aurar ragowar titi..,

ji yayi kan'sa ya sara mai shi ba mace bane balle ya iya tantance abin da innar sa take fadi amma tabbas duk abin da ta faɗi gaskiya ne shima kan'sa kyan da yumna tayi ba ƙaramin mamaki yake bashi ba sai kawai ya barshi a gyaran jikin da aka yiwa amare ne shi ya mai data haka baya zargin yumna ya yarda da tarbiyar ta amma ya ya iya mahaifiya ba wasa ba.
hawaye ne yake zubowa a idanuwan'ta tace " be kamata ba dan bakya sona kiyi min wannan ƙazafin ba , ko da ace Mamman zai sake ni karka sakeni da wannan baƙin tabon da har abada ba zai taɓa gogewa ba a idanuwana da zuciyar'ta kina da ya'ya mata kin haifa be kamata ki jefeni da wannan kalmar ba.
wata uwar buda ta saki tace " au Allah maza saketa ina gani kuma ta taso na kaita har gidan su na shedawa kowa abin da , ta aikata..,

Mamman dakyar ya iya haɗiyar yawu ganin yayi shiru innar sa ta saka kuka tare da kakorin tsine mai da sauri yumna ta girgiza kan'ta tace " Mamman bakomai karka bari saboda dani ka ɓata lahirar ka , komai me wucewa ne wallahi..,

a hankali ya furta na sake ki saki biyu..
share hawayen ta tayi ta tashi ta shiga daki mayafin'ta ta dauko ranar daurin auren ta an sake ta saki da ashe daman haka yake da ciwo ashe daman jin sa kawai take abaki amma wata zuciyar'ta ta murna take wata na bakin ciki saboda da bakin tabon da aka sake ta dashi.
a daidai nan mahaifinsa ya zo hindatu ta kira shi saboda abin da yake faruwa.
yana zuwa inna ta kora mai bayani tabbas ga amai nan amma yace " ke kin tabbatar da wannan zargi tabawa kiji tsoran Allah Ubangijin fa baya yafe hakkin wani akan wani idan kinyi haka ne domin ki tozarta su wallahi Ubangiji zai jarabbe ki ta inda ba kiyi zato ba..,
a dai-dai nan yumna ta fito tana saka mayafi mahaifinsa yace " ya'ta koma ki kwanta gobe sai mu yi magana...,
na rantse da Allah sai ta tafi ta zauna tayi me a cikin gidan nan..?,
tashi yumna tayi ko gaban ta bata iya gani ta fita Mamman kuwa ya zama tamkar wani mutum mutumi,
 dakyar take iya tafiya ikon Allah ne ya kawo ta gida amma ba dan haka ba , da tuni wani zancen ake yi malam yana zaune asoro shida mommy suma magana ta shigo da yake akwai hasken fitila da sauri mommy ya zaro idon'ta tare da dafe kirjin ta da yake dukan uku uku malam kuwa daskarewa yayi dakyar ya iya cewa yumna me ya dawo dake..?,
ɗurƙusawa tayi tana kuka tare da shashsheka ta kasa magana ganin haka mommy tace " malam mu shiga daga cikin dakin nan na zaure har yanzu akwai mutane a cikin gidan nan wasu ma kwana za su yi.
tashi yayi jikin sa duk a sanyaye ya buɗe dakin su hafizu shiga su kayi mommy ta ƙara mai maita mata tambayar dakyar yumna ta iya cewa sakina ta saka yayi saki biyu na fito ina amai tace cikine dani
salati mommy ta saki shikkenan magana ta ƙare innalillahi wainna ilaihir raji'un haka suka shiga maimaitawa mommy tace " Allah ya isa tsakanin mu da ita yarinyar da take al'ada wanne ciki insha'Allahu akan ya'yanta zata ga ciki alfarmar annabi Muhammadu Sallallahu alaihi Wasallama sai dai ta gani akan nata badai akan kiba, ni daman tun da ta iya rufe ido ta ci mana mutunci nasan bata da imani bata da tsoron Allah yanzu maganar da muke yi da malam kenan a cikin daran nan a ranar da aka daura muku aure ta saka a yi miki wannan sakin hulakancin gaskiya matar nan bata da imani ko yan baki ba su soma watsewa ba insha'Allahu yumna sai kin zama wata makaranta kawai zaki koma da zarar takardun ki sun fito ta mai dake ƙaramar bazzawara.,
malam kasa cewa komai yayi ko da ya tashi binciken Mamman da man ance mahaifiyar sa tafi karfin mahaifinsa ashe kuwa haka abin yake da ya sani ƙeya da be haɗa wannan auren ba dama ya bar yarsa tun farko da ta nuna bata so bakomai haka Allah ya tsara daman auren su na wani lokaci ne , duk da ba'a shedar ɗan yau amma yasan halin kowa daga cikin ya'yansa ita dai yumna barta da daukan magana amma wallahi baya zarginta balle gashi nan ance ma al'ada take yi wannan mata ta cuce su bakomai Allah yana nan ma dakata.
dakyar ya iya cewa yumna kiyi hakuri kiyi hakuri kiyi hakuri Allah yana tare da me gaskiya wata ran zatai nadamar abin da ta faɗa miki kafin su hafizu su zo ku tashi ku koma cikin gida..
da sauri mommy tace " a'a duk da dare yayi kawai mu koma gidana ai haka kamar tozarta kai ne..,
haka ne wallahi Allah ya rufamana asiri amin mommy tace ta tashi ta shiga yusra ta kwaso

muku kayan su suka fito daman tun ɗazu kaka ta tafi buɗe Boot tayi ta zuba kayan sannan ta rufe.
yusra ta shiga gidan gaba saboda ita zatai tukin daman ta matsu su tafi so take yi ta ganta a gidansu amma mommy tace ba yau ba sai gobe sub koma gidan yumna zuwa jibi su tafi.
tamkar an warke ta daga Makanta taga mommy ta kamo hannun yumna ta buɗe baki za tayi magana mommy ta hade rai ta buɗe gidan baya ta shiga ganin haka itama ta tsuke bakin ta kwantar da kan'ta tayi a cinyar mommy tana kuka zazzaɓin jikin'ta ya ƙara tsanani ba irin abin da yumna bata saka aranta ba wayar ta da take makale da ita a cikin zaninta ta ciro tace " mommy ajiye min..,
cikin tausayawa mommy ta karɓar ta ajiye mata ba karamin tauyasin yumna take ji ba , dan ma yarinyar tana da karfin zuciya da wata ce faɗuwa za tayi idan ta ji wannan zance.
sai karfe goma suka isa me gadi ya buɗe musu gate lokacin juraij ya dawo daga aiki shima turus yayi ganin yumna ta fito abinka da babban gida ga wadatar hasken wutar lantarki tamkar rana jikin sa a sanyaye ya ƙara so yace " mommy sannun ku da zuwa..?,
Yauwa juraij yanzu ka dawo..
Eh wallahi yanzu na dawo nama biya ta gidan su ahlam jikin nata da sauki ba kamar jiya ba.
Mommy tace " to Allah ya kara sauki nama kirata ɗazu naji ya jikin ta wayar ta a kashe..,
insha'Allahu zan faɗa mata kallon yumna yayi zai wuce mommy tace " juraij ina son ganin ka..,
gaban sane ya faɗi amma sai ya dake yace " to mommy..,
buɗe motar sa yayi ya ajiye kayan da ya dauko ya bi bayan su.
lokacin mommy ta shiga daki yusra ta hau sama domin bacci take ji yumna ce a zaune a parlour be bi takanta ba ya nufi bedroom din mommy sallama yayi tana zaune ta rafka uban tagumi sai ya ya kara magana sannan taji shi.
da sauri ta ɗago tace " juriaj ashe ka shigo,
    zama yayi a ƙasa ya tankwashe ƙafafuwan'sa yace " mommy me yake damin ki naga kin yi tagumi Allah ya saka lafiya wallahi na shiga tashin hankali sosai dana ganki a cikin wannan hali..,
ajiyar zuciya ta sauke tace " juraij wallahi ina cikin matsala kai kaɗai ne zaka iya fiddani a cikin wannan matsalar taufiq baya nan yana karatu da shi zanwa magana..,
kallon ta yake cikin mamaki domin be san ina zancen ta ya dosa ba temako kuma yau mommy ce take neman temakon sa to duk yadda aka yi ba ƙaramin abu bane wannan dan haka yace " mommy Dan Allah ki faɗa min me ke damu ba ki..?,
ajiyar zuciya ta sauke ta share kwallar da take ƙoƙarin gangarowa a kurmin idon'ta tace " yau an daurawa yumna aure a yau uwar mijinta, ta saka aka sake ta daman tun daga tarbar da tayi mana wallahi nasan ba mutuniyar kirki bace..,
gumi ne ya shiga yanko mai ya shiga uku yasan yanzu haka shi momy zata ce , ya auri yumna ba zai iya adalci ba , ba zai iya haɗa ahlam da ko wacce mace ba , ba zai iya ba ji yayi  ya shiga cikin wani irin hali wanda ya kasa fassara shi to wacce siga.
tissue ta yago ta share hawayen ta tace " kai nake da yaƙinin zaka iya riki min amana ko bayan raina ba zaka taɓa iya tozarta yumna ba , taufiq yana da wata dabi'a da wani hali ba ko wanne abu ya ke so ba , idan na tursasashi ba lallai yace min ba zai iya ba amma abin zai dinga ci mai rai ƙarshe ya haifar mai da wata lalurar kai nake da ya ƙinin za ka iya yi min wannan aikin kai zaka iya riƙe min wannan amanar duk da ba lallai ka amsa ba amma ka riƙe min ita ina so ka

aure yumna tun da be ɗora mata idda ba
habawa ji yayi tamkar an dauko ringimeman dotsai an ɗora mai akan zuciyar'sa ina bazai iya ba duk ba ba zai iya yiwa mahaifiyar sa musu ba amma ba zai iya yin adalci ba ƙasa magana yayi tun da ya sunkuyar da kan'sa ƙasa be dago ba har ta gama zancen ta bakin sa na rawa yace " mommy auren ta zanyi...?,
kai ta gyaɗa mai ,
baya son zubar hawayen mahaifansa baya son abin da zai saka tayi kuka yana da kuma maganin damuwar ta , ya saka yi mata bakin sa na rawa yace " mommy ki gafarce ni bazan iya auren ta ba , saboda Muhsin yana son ta ba zan iya zama da abin da aminina yake so ba ina da yaƙinin Muhsin zai iya riƙe wannan amanar wallahi tun da ya ganta yake min maganar ta sai da na gaji na faɗa mai an mata miji duk da haka be hakura yanzu haka yau da nake ce mai yau ake ɗora mata aure wallahi yana kwance akan gadon asibiti idan aureta ban mai adalci ba hakika na cika bakin amini wata kila ma hakan ya kawo karshen alakarmu saboda so mugun abu ne zai iya haɗa mu duk irin amintar da take tsakanin mu dan Allah mommy karki ce ban bi umarnin ki ba amma me zai hana taci gaba da karatun ta yadda zata iya dogara da kan'ta zata tallafi rayuwar maraicinta har Allah yayi abin da ya tsara..,
ya faɗa yana riko hannunta tare da goge mata hannunta.
Mommy kasa magana tayi wannan ita ake kira da tsaka me wuya taso ace yumna ta auri Juraij daman tun farko shi taiwa sha'awar'ta sai kuma ya kawo mata ahlam ba yadda ta iya ta amince da auren ta tabbas ba za ta ita tauye mai hakkin sa ba duk abin da ya faɗi gaskiya ne zata bar zancen auren nan Allah ya zaɓa mata abin da ya fi alkairi dakyar tace " bakomai wallahi Juraij Allah yayi maka albarka ya shige mana gaba daman nima cewa nayi ko a dakin mijinta ta ci gaba da karatu amma wannan abin har abada bazai bace mata a rai dan Allah ku jata a jiki ku hanata zaman kaɗaici duk abin da za tayi karku kyareta sai abu yayi mata yawa ku bita a hankali komai yana da lokaci komai zai wuce tamkar ba ayi shi ba...,
insha'Allahu ya fada yana tashi ba karamin sanyi yayi ba lokacin da ya samu nutsuwa da amincewa da tayi da maganar sa..

Copy is not allowed
Domin jin audio din Yan zaman Makkah Ku danna wannan link din sannan kuyi subscribe Dan Allah.
https://youtu.be/cDE5bjYY2HY

---

https://www.arewabooks.com/chapter?id=6817816be532b4a92550458c
Episode 13
sai da safe yayi mata ya fita har zuwa lokacin yumna tana kwance akan kujera ta , takure guri ɗaya.
wuce ta yayi ya fita tana ganin fitar sa ta miƙe ba karamin bacci take ji ba dai-dai lokacin mommy ta fito kama hannunta tayi ta kaita har dakin ta , wanda da aka sauketa a cikinsa kwanciya tayi akan gado tare da yin addu'a mommy ta ja mata kofa rufe idanuwan'ta tayi zuciyar ta na mata wani irin suya , bawai bakin ciki take da Mamman ya sake ta ba a'a daman abin da take nema kenan kuma sai ta samu, babban bakin Cikin da sharrin da mahaifiyar sa tayi mata , ba zato taji hawaye na bin kuncinta sharewa tayi ta gyara kwanciyar ta ranar yadda

taga rana haka taga dare zazzaɓi ne ya ƙara rufe ta ko iya daga idanuwanta bata yi ga ciwo da kan'ta keyi tamkar zai fashe gida biyu.
ji tayi anyi knocking kofar ta , ba damar tayi magana tayi shiru ko da aka turo kofar ko iya ɗaga kai bata yi
ashe mommy ce ,,
zama tayi a kusa da ita Alhaji yace " yumna ya jikin naki..?,
dakyar ta iya cewa Alhamdulilah da sauki..
sosai ya tausayawa yarinyar saukar sa kenan a ƙasar mommy take bashi labari shine ya shigo domin ya duba ta ,,
kwalla mommy ta share tace" Alhaji anya kuwa ba za'a kaita asibiti na , jikin nata yayi tsanani..?,
Alhaji yace " tun da ga taufiq nan ya dawo, ya duba ta da ace juraij be tafi wajen aiki ba da shi ya kamata ya duba ta tun da daman ɓangaren mata ya karanta.
 ajiyar zuciya ta sauke tace " to bara na kirawo shi Allah ya saka be kwanta wannan shegen baccin nasa ba , yawa na mutuwa..,
zauna ki kula da ita,zan kirawo shi
to tace ta shafa kan yumna da yayi zafi raɗau tamkar garwashin wuta.
 cikin tausayawa tace " yumna sannu me yake damun ki..?,
kasa magana tayi sai bakin ta da yake rawa alamun tana so tayi magana ba halin yi hawaye mommy ta share mata , tace " kiyi hakuri akwai Allah, komai yayi zafi maganin sa Allah..,
kai kurum ta gyada da kyar, ta riƙo hannun mommy Assalamu alaikum..
da sauri mommy ta juyo jin muryar taufiq tace " wa'alaikas'salam..,
ƙarasa shiguwa yayi yana cire medical glasses din'sa yace " wannan ce mara lafiyar..?,
mommy ta kalle sa tace " eh..,
dan jim yayi sannan yace " mommy ban tawo da komai ba ko , kayan sawata ban tawo da su ba , tun da na san ina dasu anan sai dan abinda zan yi amfani dashi, dashi na tawo , ko za aku kaita asibiti naga jikin nata yayi tsanani..,
tashi mommy tayi tace " dauko mota ka kai mu..,
to yace ya fita Alhaji ya ci karo dashi yayi mai bayani yace to ba damuwa ya dauko ya kai su bayan ya gama dai-dai ta parking din'sa, ya dawo daukan ta yayi domin ba zata iya tafiya ba har cikin mota ya saka ta mommy ta shiga suka fati kai tsaye asibitin da yaza mo mallakin juraij wato J.M international hospital suka isa cikin gaggawa suka amshe ta saboda yanayin jikin nata kai tsaye emergency room suka shiga da ita.
mommy jin gina tayi da bango taufiq yace " mommy me ya haddasa mata wannan ciwon ne..? , zama tayi akan waiting chair tace" taufiq labarin yana da yawa mudai samo kan'ta sai nai maka bayani..,
jan bakin sa yayi ya tsuke ya zauna kusa da ita.
Wannan kenan
AGADEZ
karfe goma malam ya shirya domin zuwa gidan su Mamman yaji ba'asin abin da ya faru har kawo i yanzu ba wanda yasan me yake faruwa da yaji nazeefa tana cewa zata gidan yumna hanata yayi yace shi baya son irin wannan daga yin auren har zata fara sintiri ko gidan shamsiyya be yarda ta je ba.

yana gama fadar haka ya fice kai tsaye gidan su Mamman ya nufa bayan ya isa ya aika yaro ace yana sallama da mahaifin Muhammadu..,
shiga yaron yayi ya fara rangaɗa wata uwar sallama yace " wai inji malam NURA me sittin yana sallama da baban Muhammadu..,
Innar su hindatu da take gaban wuta tana dumamen tuwo tace " je ka , kace mai baya nan..,
da sauri sarkin fawa ya fito yana cewa haba tabawa me ya saka kike haka ne tun da dai kin raba auren nan hankalin ki , ya kwanta ai sai ki ci wake ki sha ruwa kaf garin nan ana darajja malamin nan amma shi ne kika ce a faɗa mai haka..?,
tamkar da dutsai yake magana bata dago Kai ta kalle sa ba girgiza kai yayi ya fita yana saɓa babbar riga a kafaɗa.
samun malam yayi yana tsaye a kofar gidan nasa gaisawa sukai sannan yace " bisimallah shigo zaure...,
Malam yace " a'a barshi nan ma ya isa..,
Allah annabi yayi mai sannan ya shiga ba yadda ya iya daduma ya shinfida mai suka ƙara gaisawa sannan malam yace
" naji wani abu to domin na tabbatar shi ne na zo naji gaskiyar magana me ya faru yumna tace min Muhammadu ya sake ta..?,
kunya ce ta rufe Sarkin fawa kan'sa yana ƙasa yace " to, haka Allah ya nufa daman auren ba me dadewa bane, mahaifiyar sa , ce tace ya saketa wai saboda ta shigo mai gida da ciki Allah shi ne masani wallahi dole tai mai ya sake ta , ba yadda ya iya , wallahi nauyin ka ne ya hani zuwa na same ka mu tattauna amma insha'Allahu zan wa tubkar hanci da yardar Allah zata dawo dakinta saki biyu yayi mata , abin da nake zargi daman bata son ta shi ya saka tayi mata wannan sharrin..,
kai kurum malam ya jinjina yace " Allah ya saka hakane yafi alkairi bakomai Allah zai fitarwa da kowa hakkin sa alhamdulilah tun da kun gane ba haka bane ba damuwa ,ko za ku iya bani takardar ta..,
dan Allah kayi hakuri nasan ba akyauta muku ba wallahi ba yadda zanyi cewar sarkin fawa.
murmushi malam yayi har yanzu kamilar fuskar sa bata nuna damuwa ba ko ɓacin rai yace " ba damuwa Allah ya yafe mana baki ɗaya..,
godiya yayi mai ya ci gaba da cewa bara naje na saka shi ya rubuta takarda.
to malam yace mai yana jiran sa be jima ba ya fito amsa yayi, yayi mai sallama ya ta fito yana tafiya tana zancen zuciya abin duniya duk ya ishe shi, maganar mutanen gari ma ta ishe shi, ace aure daga kwana ɗaya anyi saki to bakomai yasan Ubangiji jaraba shi yayi ya gwada imanin sa , Allah ya bashi ikon cinye wannan jarabawar har ya isa gida be dena tunani ba.
koda ya isa a waje ya zauna yana karatu almajirai suka zauna yana karbar haddar kowa tare da ƙara musu wani sosai yaji  zuciyar sa tayi sanyi tabbas Alkur'ani waraka ne , maganin damuwane al'ummar annabi mu dage da ibadar Allah.
ko dan muga haske a cikin rayuwar mu.
#####
Sai karfe 1:40 aka fito da ita an saka mata oxygen sannan an ɗaura mata drip a hannunta kai tsaye daki suka shiga da ita mommy za tabi bayan su taga Juraij ya fito ashe dashi aka shiga ba ƙaramin mamaki tayi ba da ganin sa da tayi saboda ɗazu bata ga an shiga da shiba tace " juraij daman kana ciki..?,

cire glove yayi  matsawa yayi kusa da wani automatical dustbin tuni ga buɗe ya jefa su yace " kirani su kayi akwai wata kofa a baya tanan na shigo..,
nifa ince ya jikin nata..?
juraij yace " da sauki damuwa ce tayi mata yawa amma insha'Allahu zuwa anjima zata warware..,
to Allah ya yarda mommy ta faɗa tana shiga world din da aka kai yumna tura kofa tayi taufiq ne zaune yana danna waya zama tayi a kujerar da take facing din sa tace " bata farka ba ko..?,
ɗagowa yayi ya kalli yumna da take kwance yace " a'a ko motsi ba tayi ba , amma wani likita yace min sai nan da karfe biyar zata farka sun mata allura ne..,
ajiyar zuciya ta sauke tace " Allah ya kai mu darai da lafiya..,
amin ya Allah ya faɗa yana tashi zura wayar sa a aljihunsa yayi yace " mommy ni zan tafi zan turo miki yaran nan sa taya ki zama wallahi wani irin bacci nake ji duk na gaji..,
Wallahi kuwa akwai gajiya yau ka sauka kuma kuma baka huta ba , Allah dai yayi albarka sai dai in yusrah juhud yanzu haka nasan ta , tafi gurin aiki, itama yusrah ko ta tafi makaranta Allah masani.
Cikin kaunar mahaifiyar tasa yace " amin ya Allah to zan dai duba na gani duk abin da ake ciki za kiga nayi miki waya ya jikin ahlam..?,
mommy tace " da sauki hice ko ka kirawo ta..?,
shafa sumar kan'sa yayi yace " eh na kirawo ta maman su ce ta ɗauka tace tana bacci amma zata faɗa mata..,
To Allah ya ƙara sauki ciki ne me laulayi ga haɗo da rashin lafiya kullum ba lafiya wallahi tun ina ganin yarinyar nan lanjarewa take har kuma naga ashe ba lanjarewa take ba cutar ce Allah dai ya raba lafiya haka wani cikin yake sai ranar da aka sauke shi ake samun sauki
amin ya Allah yace yana fita daga cikin dakin.
AGADEZ
kamar ance mai ya ɗaga idanuwan'sa ido hudu yayi da zaliha jikar hajiya rakiyar mahaifiyar marigayya da flask a kanta da wani a hannunta gaban sane ya fadi bayan shi da Hajiya zainab ba wanda yasan da mutuwar auren yumna ba mamaki abinci tayiwa yumna za akai mata gidan ta ,
share zuba yayi be san ya zai yi ba , baya so mutuwar auren yumna ta fito yanzu duk da yasan koman daren dadewa dole abin ɓoye ya fito sarari.
shiru yayi yana tunanin mafita duk hanyar da yabi sai yaga ba me bullewa bace baya so hajiya tasan da zancen nan kodan shekarunta sun ja zata iya shiga ko wanne hali.
yana cikin wannan tunanin zaliha ta ƙaraso ba zato yaji tace " malam ina wuni..?,
wani irin dam kirjin'sa yayi dakyar ya iya dagowa ya kakalo fara'ar dole yace " lafiya qalau ya jikin Hajiya..?,
zaliha tace " alhamdulilah wallahi da sauki ɗazu ma ta sha magani, abinci tace na kawo idan akwai wanda zai ke gidan aunty yumna sai mu tafi tare da shi..,
Malam yace " to masha Allah, Allah ya ƙara sauki a'a ba wanda zai je, amma kawo a ajiye idan akwai me tafiya sai na bashi ya kai mata kice ina godiya, ina yi mata kuma ya gajiya..,
ajiyewa zaliha tayi tace " to insha'Allahu zan faɗa mata..,
kuɗi ya ciro a aljihunsa ya miƙa mata kin amsa tayi sai da yayi mata jan ido sannan ta amsa tana yi mai godiya ta bar gurin.

#########
Misalin ƙarfe biyar dai-dai yumna ta farka buɗe idanuwan'ta tayi lokacin mommy da su juhud suna hira a hankali ta saka hannu ta cire oxygen din da aka saka mata da sauri mommy ta tashi tana cewa a'a yumna karki cire.
tashi tayi dakyar tace " mommy mu tafi gida naji sauki..,
yumna ya jikin naki..?
cewar taufiq da yake facing din ta da sauri ta ɗago jin wata murya da ba , taɓa jin ta ba kallo ɗaya tai mai tasan dan mommy saboda kamar da taga yana yi da ita a hankali tace " da sauki..,
TAUFIQ yace " Allah ya ƙara sauki...,
jingina tayi a bango tace amin..
mommy tace " taufiq kirawo JURAIJ kace ta, tashi..,
tashi yayi yace " to..,
fita yayi kai tsaye office din Juraij ya nufa sai da yayi knocking sannan ya bashi izinin shugowa shiga yayi ya zauna a kujera yace " yaya yumna ta tashi yanzu tama cire oxygen din da kuka saka mata..,
kwafa yayi yace " yarinyar nan bata ji wallahi daman nasan zata iya aikata haka ...,
yaya wai me ya faru da ita ne har ta shiga wannan hali..?
cewar taufiq.
Juraij yace " nima ban sani ba ka tambayi mommy mana..,

Copy is not allowed 🚫

Domin jin audio din Yan zaman Makkah Ku shiha wannan link din sannan ku danna min subscribe Dan Allah.

https://youtu.be/cDE5bjYY2HY

---

https://www.arewabooks.com/chapter?id=6817816be532b4a92550458c

Episode [13]

Hmm tace min sai ta gama warware wa zatai min bayani abin da yake faruwa.
tashi juraij yayi yana cewa amma kazo kana tambaya ta , ashe ma tace zata baka labari har yanzu baka dena halinka ba nason jin zance ni wallahi dama karatun jarida su mommy suka tura ka ba karatun likitanci ba domin dashi ya dace dakai.
dariya taufiq yayi yace " wallahi kawai abin ne ya dame ni shiyasa nayi magana yarinyar ta shiga raina, musamman ma dana ji saboda damuwa ta shiga wannan hali ta ban tausayi da shekarunta kanana ta faɗa irin wannan hali..,
hmm kawai juraij yace domin taufiq be san wace yumna ba amma Allah ya bata lafiya kwana ɗaya za tayi ya fahimci wace ita daukan folder yayi yace " taufiq zaka zauna ne na je na dawo ko kuwa fita za muyi tare..?,
tashi yayi yace " a'a yanzu zan tafi sai kuma gobe insha'Allahu zan dawo naga ya jikin'ta yake..,
okay kawai yace tare suka fita wata nurse ta bi bayan'sa yana shiga mommy na lallabata ta ci

abinci takaici ne ya ishe shi ji yayi kamar ya buge ta sai wani shagwaɓa take yi mommy na biye mata Allah ne kaɗai yasan me tai wa mijinta ya sake ta shikkenan ta cuci kan'ta, ta zama ƙaramar bazzawara ƙara tamke fuskar'sa yayi domin baya son raini...
jan kujera yayi ya zauna yace " mommy barka da yamma..,
cikin kulawa mommy tace " barka dai ashe ya fada maka..,
m
Eh ya faɗa min ya faɗa yana buɗa folder din yumna batare da ya kalle ta ba yace " ya jikin naki dame dame kike ji a jikin ki..?,
dauke kai tayi tace " na samu sauki ni ka sallame ni..,
ji yayi kamar ya buge ta amma sai ya danne yace " tambayar ki nayi me kike ji a jikin ki..?,
ɗauke kai tayi ranta duk a ɓace tace " nace maka na samu sauki fa..,
ajiyar zuciya ya sauke yace " okay..,
ajiye folder din hannunsa yayi ya soma haɗa allura gaban tane ya faɗi ba abin da , ta tsana sama da allura har gwara magani tana iya sha idanuwanta ne suka fara kawo ruwa zuciyar ta , ta fara rawa tamkar zata faso kirjinta ta fito tace " mommy ki yi mai magana nafa ce mai na samu sauki amma kinga yana haɗa allura..,
mommy tace" haba yumna ya zan shiga aikin sa, bakya so ki samu lafiya sosai kinga fa kwana biyu duk kin rame..,
haɗe rai tayi zuciyar ta ba dadi wato itama mommy ta goyi da bayan sa ai kuwa ba allurar da zai mata kallon sa tayi tace " ya Jawad cire min ƙarin ruwan nan zan shiga bayi..,
be nuna ma yaji me take cewa ba , balle ta saka ran zai amsa mata ranta ne ya ɓaci tana wannan tunani sai ji tayi ƙarar shigar siriji a dantsan hannunta za bura za tayi tuni ya riƙe ta ya hanata ko da motsi sai da ya gama yi mata tas, sannan ya saka audiga a gurin yace " ungo ki danne ta kar ta zame miki ciwo..,
idan ta tanka shi to bango zai magana ganin haka ya saki murmushin mugunta karfin zuciyar ta yana bashi mamaki ta rasa da wa za ta dinga faɗa sai dashi yau zata gane kuranta,
dannawa ɗaya yayi mata sai da kashin ta ya amsa cike da mugunta yake mulmula mata gurin , kuka ta saki amma be saurara mata ba har sa da yaga jikin'ta yayi laushi sannan ya barta.
daukan folder yayi, yace " mommy sai da safe..,
Mommy tace " yau da wuri haka zaka tashi..?,
Eh wallahi ina so na biya gidan su ahlam na ƙara ganin jikin ta.
to Allah ya ƙara sauki
da sauri yusrah tace " yaya zan bika daman yanzu nake shirin tafiya gida..,
juraij yace " to tashi mu tafi...,
Juhud ta gallamata harara tace " ni kuma ce miki aka yi ba tafiya zan yi ba ,
yusrah tace " ai na zata da yaya taufiq za ku tafi ne shi ya saka ban yi zaton tare za mu tafi ba, baki tawo da motar ki bane..?,
Mommy tace " tuni taufiq ya tafi gida..,
mommy ke kika bata amsa a gaban ta ya TAUFIQ yayi miki sallama yace amma shine take wannan maganar sai kace wacce ta sha kwaya
juhud ta faɗa cikin zafin rai
Dafa ta yusrah tayi tace " Allah ya baki hakuri...,
ganin zai tafi ba abin da kuma yace da sauri tace " ya Juraij baka sallame ni ba, nace maka naji

sauki...,
wani kallo ya yi mata tuni ta hadeyi sauran zancen ta wannan kallo da yayi mata ba ƙaramin nutsar da ita yayi ba , kowa shakkar sa yake amma ita ce take ma iya musayar yawu da shi, saboda zafin sa bama ya shiga sabgar mutane musamman wanda yasan zai raina shi.
bayan fitar su malam ya kirawo Hajiya da sauri ta ɗauka suka gaisa yace '' na karbo takardar ta saki biyu ne , ɗazu Hajiya ta kawo mata abinci to wallahi ban san yadda zan mata bayani ba kinga har yanzu na rasa nutsuwata bana so mutuwar auren yumna ta baza ko ina bana so a sani..,
ajiyar zuciya ta sauke tace '' wallahi nima yau haka na yini cikin tunani ko wacce hanya nabi sai naga ba me bullewa bace ba , ga jikin hajiya bana so ta sani kar jikin'ta ya ƙara rikicewa azo a haifi da mara ido...,
malam yace '' nima abin da nake jimami kenan wallahi..,
mommy tace '' to Allah ya shige mana gaba wallahi matar nan Ubangiji ba zai taɓa barin ta ba da nayi ƙoƙarin daukan mataki sai kuma na gani idan na dauka tamkar na daɓawa kan mu wuƙa ne
za a san me yake faruwa bayan so muku wannan sirrin ya rufu ba wanda zai ji shi nan kusa..., tabbas haka ne amma ba yadda muka iya wata ran dole a sani Allah dai ya shige mana gaba.
amin ya Allah mommy tace
kwanan yumna biyu ya sallame ta saboda jikin'ta yayi kyau taji sauki a lokacin ma ahlam ta dawo sosai suke takun saƙa da ahlam tambayar duniya ahlam tayiwa juraij wai fasa bikin akai ko kuma wani abu ne ya faru amma yayi mata banza baya ma tanka mata.
hakan da yayi ba karamin fusata zuciyar ahlam yayi ba ji tayi ba wacce ta tsana a duniya sama da ita tsoran ta ɗaya kar juraij yace yana son ta
tunda ta lura duk abin da ake so a jikin mace ta haɗa shi , ita da take da aure ma tafi ta komai to halin namiji ba tabbas duk irin son da yake mata zai iya sakawa idonsa toka yace labari ya canza.

da taga suna mutunci da taufiq sai hankalinta ya dan kwanta ko kaɗan bata so wato kishiya.
Yau ranar Litinin yusrah ta tafi makaranta juhud wajen aiki taufiq ma ya bi juraij asibiti daga ita sai mommy sai masu aiki rasa yadda za a yi tai wa mommy karya ta barta ta fita, dan a kwana kusa take son barin kasar niger ta tafi makka.
tana cikin wannan tunani saliha me aikin su ta ajiye mata lemo tace '' gashi nan..,
ɗauka tayi ta buɗe ta fara sha ba tare da tace komai ba kwata kwata tunaninta baya kan su yana wani guri can daban hakan da saliha ta gani ya saka ta zauna kusa da ita tace '' yar nan tunanin me kike haka ..?,
da sauri ta ɗago saita kan'ta tayi tace '' bakomai bana son magana ne baba saliha kaina ke ciwo..,
dafa kan'ta tayi tace '' ayya sannu Allah ya baki lafiya kin faɗawa hajiya..?,
yumna tayi kallar tausayi tace '' a'a ban fada mata ba , bana so hankalinta ya tashi ..,
Baba saliha tace
''gaskiya kinyi kyan kai tunda na lura kamar kwana biyu hajiya na cikin damuwa
bara na kawo miki magani ki sha za kiji sauki..,,
da sauri ta kalle ta , tace '' a'a barshi nagode nan da anjima insha'Allahu zai saki..,

dariya tayi tace " bakya son Shan magani Allah ya shirye ki..,
shiru tayi mata tabar gurin da sauri ta ajiye lemom hannunta ta shiga dakin mommy samun ta ,
tayi tana danna waya zama tayi a ƙasa tace " mommy barka da wannan lokaci..,
mommy tace " barka dai yumna ya jikin naki...,
ƙasa tayi da kai tace " na samu sauki..,
to masha Allah
wasa ta fara da mayafin'ta tace " mommy Dan Allah ina so naje gidan su wannan kawar tawa yau ba kowa a gidan bana so na fara wani tunanin da zai ƙara kaini da kwanciya asibiti..,
murmushi mommy tayi tace " to ba damuwa amma karki dade kinji..?,
tashi tayi tana murna tace " to..,
da saurinta ta fita daki kawai ta shiga ta dauko wayar ta da takalminta sannan ta fita tana fita ta danyi nisa sannan ta kirawo number wannan mutumin sai dai har ta katsai be ɗauka ba ci gaba tayi da tafiya tana kiransa sai da ta zo gab gurin sannan ya ɗaga kiran ta lokacin tai mai kira kusan goma sha ,
da sauri ta kara a kunne tace " yallaɓai gani nan ina bakin gate din ku na farko yau nazo a yimin komai da komai..,
Mutumin yace " to masha Allah kin kuwa yi sa'a wannan satin zan mu kai wasu kinga sai a saka har dake a ciki tunda kin dade da yin booking..,
wani dadi ne ya kamata tace " kai amma naji dad'i Nagode Allah ya ƙara arziki...,
ba damuwa ki shigo muyi maza muyi abin da za muyi lokaci yana kurewa dan gani nake na za'a ƙara kwana biyar ba za ku tafi...
ba ƙaramin dad'i yumna taji ba da wannan zance jin kanta tayi a sama shiga gate din tayi tana rarraba ido can ta gani office din nasa,
da sauri ta ƙarasa knocking tayi sai da ya dan jima sannan ya buɗe mata samin wata mace tayi daga, ganin ta yar duniya ce amma ba zata wuce sa'ar ta ba idan ma ta girmeta kaɗan ne sallama tayi ta juyo ta ƙarewa yumna kallo sannan ta amsa cikin fara'a.
yumna ma ganin bata ja mata aji ba sai ta saki jikin ta tace " ina wunin ku ina gajiya..,
amsawa sukai da lafiya qalau wannan matar tace " sunana bintu mukhtar maradi..,
murmushi yumna tayi tace " ni kuma yumna nura Agadez..,
kai bintu ta gyaɗa tace " kin sha hanya..,
murmushi kawai yumna tayi ta mai da hankalin'ta kan mutumin nan tace " nice wacce mukai waya yanzu..,
dariya yayi yace " na gane ki yanzu za ayi komai..,
ba karamin dadi taji ba ai kuwa ba ɓata lokaci yayi mata komai bayan ya gama nasa ya turata office office ta cike takardu tare da saka hannu visa ma anan akai mata abin ka na kudi komai a ranar aka gama yi mata duk wani chuku chuku suka bata set number ta ashe itama wannan tafiya za tayi tare da ita akai musu komai ita da yumna sukai chanzan number sannan sukai sallama yumna ta kamo hannyar gida tun karfe biyu ta fita bata dawo ba ,
sai biyar tana shiga mommy ta fara yi mata faɗa tace " haba yumna haka mukai dake wallahi ban ji dad'i ba , yanzun nan malam ya fita daga gidan nan duk da be nuna min wani abu a fuskar sa ba amma nasan ba zai ji dadi ba , tas an kwaso kayan ki, wannan shegiyar matar ta cuce mu wallahi yawo take tana cewa cikin shege kika yi labari duk ya baza gari..,
zaman yan bori tayi bawai dan abin ya dame ta ba a'a sai dan kawai sun kyale ta, ta yi tafiyar

ta.
kuka ta rushe dashi mommy komawa tayi tana lallashin ta tare da bata baki amma ƙememe taki yin shiru ta ci gaba da kukan ta zuciyar'ta fes idan bata nuna ta damuwa ba,
ba zata iya zama a kusa da mutane ba zata ƙeɓe kan'ta zuwa na ɗan wani lokaci tasan ba zasu barta ba , ta sarara dan haka wage baki tayi tana ta kuka har da shashsheka rarrashin duniya mommy tayi mata taƙi yin shiru.
tamkar zugata tayi ma,
sai da tayi me isarta sannan tayi shiru tace " mommy yanzu wanne kallo mutane za su yi min wallahi mommy bazan iya komawa Agadez ba , mommy Dan Allah ku barni nayi nisa da ku, zuciya ta ko zata samu sukuni bazan iya cire kaina daga cikin wannan zargi ba har abada mutane da abin za su dinga kallo na ranar da aka daura min aure ranar aka sake ni, sauka ƙasa tayi ta haɗa hannuwanta guri ɗaya tace " mommy Dan girman Allah ku barni nayi nisa da kowa ko hankali na zai kwana dan da ɗan wani lokaci nasan zan dawo dai-dai Wallahi bana son zama a kusa da wanda na sani dan girman Allah ku barni na tafi makka ko na rabin shekara ne sai na dawo lokacin nasan mutane sun riga da sun manta da abin da ya faru nima na manta da shi..,
da sauri mommy ta kalle ta cikin mamakin abin da yumna ta faɗi tace..

Ku hanzarta yin payment sauran pages biyu na gama free book 1

Book 2 500

Ne idan ya zama document ya koma 1000
Karku ce ban faɗa muku ba

Domin biya

8141785374

Amina alhasan Muhammad opay
Ku turo da shedar biya ta wannan number
08141785374
Receipt evidence kawai nake so idan kika turo na saka ki a group
bana son wannan tambayar nawa ne bayan kin karanta na baya kinga abin da na saka

YAN ZAMAN MAKKAH

OUMYASMEEN

BOOK 1

Copy is not allowed 🚫
Domin jin audio din Yan zaman Makkah Ku shiga wannan link din sannan ku danna min subscribe Dan Allah.
https://youtu.be/cDE5bjYY2HY

---

https://www.arewabooks.com/chapter?id=6817816be532b4a92550458c
Episode [15]
YUMNA kinsan kuwa me kike faɗa..? anya kuwa lafiyar ki qalau..? karma ki sake malam yaji wannan maganar, dan wannan abin ya faru sai tunanin ki ya gushe kim bawa mutane ma damar su faɗi duk abin da suka ga dama..,
kuka ta ƙara rushewa dashi tace " mommy ke uwa ce nasan zaki san irin radadin da nake ji cikin zuciya ta , mommy bansan ina zan saka kaina ba. kaɗai ci nake so wallahi a yanzu bana kaunar kowa ya raɓe ni mommy ku tausaya min ku fahimce ni nasan abin da kuke gudu, anan ma banyi ba sai a can da bani da kowa garin da ba nawa ba kowa abin da yake ransa shi yake aikatawa..,
zama mommy tayi jikin'ta yayi sanyi tausasa muryarta tayi tace " yumna ki fahimci abin da nake so ki fahimta, zaman ki anan shine rufin asirin ki wallahi bar ganin wa'yanda suke can suna baki sha'awa baki san rayuwar da suke ciki ba kiyi fatan Allah ya azurta ki, ta hanya me kyau ki tsaya kiyi karatu Allah ya fito miki da miji kiyi aure wallahi yumna duk inuwar da kike gani kina hangen ta , to ƙuna ce ba ko wacce inuwa bace inuwa wata zafin ta , yafi na rana akwai dana sani a cikin'ta mara amfani ba zaki gane wannan zancen nawa ba sai nan gaba , wani ma idan kin dawo kallon da zai miki daban har sai kin gwammace kiɗa, da karatu..,
share hawayen ta tace " mommy a tunani na zaki fahimci inda magana ta , ta dosa mommy komai yayi min zafi..,
shiru mommy tayi domin abin yumna ya fara bata tsoro ganin haka yumna tashi tayi, ta tafi dakin ta turo kofar tayi ta murza key, zama tayi a kan gado ta zuba ta gumi tabbas idan ba tai musu wuta wuta ba to wallahi ba za su yarda da wannan tafiyar tata ba ɗaukan waya tayi, ta nemi number Na'ima har ta katsai ba'a dauka ba dogon tsaki taja ta ajiye wayar a fili tace " ke daman tsiyar ki, kenan ai ta kiranki a banza..,
kwanciya tayi tana , ta wassafe wassafe a zuciyar ta , limshe idanuwan'ta, tayi tasan yanzu ba za su taɓa fuskanta ta ba , sai lokacin da nasara ta zo mata yanzu kowa kallon bai bai zai mata idan kuma nasara tazo sai a dinga dama nice, sun manta a baya abin da suka ce tabbas me hakuri yana tare da nasara zata shanye komai zata dauki komai tasan wannan duk abin taki ake zuba mata.
bacci ne ya dauke ta kiran sallar magariba ne ya tashe ta, tashi tayi ta dauro alwala ta , tayar da sallama bayan ta idar ta ƙara jaraba number Na'ima still bata dauka ba message ta rubuta mata tace " Assalamu alaiki Na'ima ban yi fushi ba , na kira ki amma ba kiyi picking call din ba na bugo ne na sanar dake nima ina nan tawowa, ki turo min sunan unguwar da kike zan kawo miki ziyara sannan ina godiya da yi min hanyar tafiya makka da kika yi Allah ya bar zuminci..,
turawa tayi ta ajiye wayar ji tayi ana knocking din kofar dakin ta banza tayi domin hausawa sunce da zafi zafi ake bugar ƙarfe..,
ko da yusrah ta gama bugunta bata buɗe ba sai ta juya ta tafi gurin mommy tace " mommy taki budewa..,

tana faɗar haka ta zauna ajiye chokalin hannunta tayi tace " to bara naje naga ko lafiya..,
Juhud da take operating system din'ta ta ɗago tace " mommy sai kace wata yarinyar karama ki kyale ta idan ta gaji zata fito ne ita fa bari ba shegiya bace da uban'ta amma zaki damu kanki..,
shiru mommy tayi ta bar gurin ƙara zuwa kofar dakin yumna tayi, ta fara bugawa still tai mata shiri hakura tayi ta barta.
bayan sallar isha ta kwanta tana addu'ar Allah ya fahimtar da yumna gaskiya.
Wasa wasa ƙaramar magana tana ƙoƙarin zama babba yumna har washegari bata fito ba Alhaji ma yayi mata magana taƙi buɗa kofar gashi aranar taufiq zai koma Ingila acan yake karatun sa tafiya su kayi rakiyar sa zuciyoyin su duk ba dad'i.
a bangaren yumna kuwa itama ba  ƙaramin buguwa tayi ba kwana ɗaya da rabi da tayi ba abinci.
    bayan tafiyar su fitowa tayi a wahale ta dade a kwance a parlour yawa wata matacciya haka suka shigo suka ganta da sauri mommy ta ɗagata numfashin'ta sai kaiwa yake yana komowa cikin sauri tace " juraij zo ka duba min yarinyar nan sakin jikin ta tayi hakan da tayi ba ƙaramin daga hankalin su yayi ba , ban da juhud da juraij ko a jikin su mommy taɓa kirjinta tayi numfashin ta sai kaiwa yake
yana komowa zama Alhaji yayi yace " to ku kuyar da mana ku bita da addu'a, Allah ya tsare ya kare ba wayon mu ba ba dabarar mu ba Ubangiji shi yake tsarawa yake kuma ikon sa..,
jikin mommy yayi sanyi tace " Alhaji mu bar wannan maganar za muyi ta , juraij wai ba magana nake maka ba ..? ka mai dani yar iska yawa da dutsai nake magana..,
Mommy yarinyar nan ku barta duniya ce ɗaga hankalin da taga kuna yi shi ya saka take wani abin tana nan ma anyi mata wannan sharrin balle ta tsallaka wata ƙasar.
cewar Juraij ran mommy ne ya ɓaci da jin wannan maganar juraij dan haka tayi shiru bata ce mai komai ba.
runguma ta , tayi, tana yi mata addu'a
ko Allah zai saka zata dawo dai-dai.
ranar yadda mommy yaga rana haka ta ga dare washegari malam ya zo tun da mommy take mai bayani yayi ƙasa da kan'sa Alhaji na gurin shi daman Juraij yana gurin aiki .
Mommy ta ƙara da cewa kawai mu barta sai a tayata da addu'a dan yau ne ka haife shi baka haifi halinsa ba zan yi magana ma da hajiyar mu itama nasan ba zata ki ba , kuma da alama duniyar ce tai mata zafi take ƙoƙarin barin gurin da aka santa duk ranta hankalin'ta ya dawo jikin'ta zata dawo gida zata waiwayo mu, idan muka matsa abin da zai faru yafi na yanzu dan zata iya illata kan'ta idan haka ta faru wa za'a zaga mu ne a ciki..,
Alhaji ma yace " nasan da ciwo dukkan mu ba haka muka so ba amma tun da , tace ita ga abin da ta za barwa kanta shikkenan ga hanya nan Allah ya bata sa'a iya gata muna yi mata ko da ace ba zata zauna a can agadez ba to ga nan, nan ta zauna ta ci gaba da karatunta har Allah ya fito mata da miji tayi auren ta amma ya kanne idanuwan'ta ta toshe kunnuwan'ta, bata tunanin wannan ɓacin rai da ta saka mu zai iya zame mata matsala a rayuwar ta sufa iyaye ba abin wasa bane , ba lallai bane wata ran ta budi ido ta gan mu, a lokacin kuma sai tai ta cizon yatsa tana dama nayi kaza , dan haka kawai kayi hakuri wannan ita ce jarabawar ka , dan kana malami ba wai ana nufin cewa ba za'a jarabe ka ba a gwada imanin ka wannan abin nasan ka sani ƙara tuna maka nake malam...,
ajiyar zuciya ya sauke ya ɗago idanuwan'sa yace " taje na barta..,

hamdala su kayi duk da sun san bawai dan yana so ba kawai ba yadda ya iya ne
hamdala yumna tayi a ranta duniya zata koma mata sabuwa bayan sallar la'asar sallama yayi musu ya tafi tare da cewa kawai baya bukatar ta ƙara zuwa Agadez ya yafe daga nan tayi tafiyar ta ,
ko a jikin'ta haka tace " to malam Allah ya kiyaye hanya..,
be ce mata komai ba ya fice daga dakin ranar haka ta wuni cikin jin dad'i farin ciki ba'a magana duniya tayi mata dadi sai shirye shirye take ba ruwanta da haɗa ran da su juhud suke yi mata juraij kuwa yafi kowa yi mata kallon banza abin da tayi ba ƙaramin ɓata mai rai tayi ba murmushi take yi ta wuce ta bashi guri
Washe garin
da za su tashi tana tsaye a harabar gidan tana shawagi da yake garin yayi limshi alamar ko wanne lokaci ruwa zai iya tsugewa a guje motar sa ta shigo ko dai-dai ta parking din'sa be yi ba ya fito cikin sauri kusan dariya ce ta kusan kubbucewa yumna ganin yana sauri kamar zai tashi sama bin bayan sa tayi da kallo ta taɓe baki tace " a haka zaka ƙare mijin tace duk ka wani firgice ɗan kadangaren da na saka mata a tsakar daki shi ne take zunduma wannan ihun wallahi kaɗan kuka gani tun da ni zaku tsana akan nace zan je na nemo arziki kamar kowa..,
be dade ba ya fito yana kwalawa masu wanki da guga kira cikin badda kama ta karaso kamar bata san me ya faru ba tace " yaya lafiya naga hankalin ka a tashe..? ni fa wallahi ban iya zaman gaba, ba..,
tamkar ya ɗora mata ashar sai kuma su yaga rashin dacewar haka tunda wanda ya kula ka , ai daraja da dashi sannan kuma tabbas ba kyau zaman gaba yace " wallahi kadangare ahlam ta gani a kusa da ita , ta kirani ni, tace kamar ta ga wulgawar mutum to sai dai kallo take bata gama tantance mene bane sai taga kadangare yana yawo...,
zaro manyan idanuwan'ta tayi ta ɗora hannu aka tace " innanallahi wainna ilaihir raji'un amma dai ba abin da yayi mata..?,
banza yayi mata ganin masu yi musu wanki da guga sun ƙaraso yace "dan Allah mati Ka iya fitar da kadangaren..?,"
kallon kallo suka shiga tsakanin mati da Haruna dakyar mati ya iya cewa wallahi oga ko son ganin shi, bana son yi ai wannan muguwar halitta ce..
innanallahi wainna ilaihir raji'un amma dai mati wallahi kun bada maza kuna maza kuna tsoran kadangare..
ta faɗa tana kallon juraij domin ta yi haka ne da biyu
aikuwa ya gane sarai ita daman ba'a zaman mutunci da ita sai anyi na tsiya juyowa yayi yace " dan ubanki shige muje ki ɗauke shi..,
Zaro manyan idanuwan'ta tayi ta nuna kirjinta tace " na shiga uku ni, ku, kuna maza baku ɗauke ba sai ni gaskiya ba zan iya ba..,
Haɗe rai yayi yace " shige mu tafi ko na kwarfe ki..,
ƙara kallon juraij tayi a karo na biyu tace " sai kace wata ruwa zaka ce zaka kwarfe ni..,
kallon su mati yayi yace " ku koma bakin aikin ku..,
To suka ce masa suka juya suka tafi yumna tana cikin tunani , bata ankara ba taji ana janta tamkar kayan wanki.
Ihu ta shiga zab gawa amma ko a jikin sa sai da ya dangana ta da parlour sa fisge hannun ta tayi tace " wallahi abin da kake baya dacewa kai , ka kasa sai kace ni nayi..,

Mari zai zabga mata ƙadan gare yayo kan'su da gudu suka , fita har da ahlam yumna tsayawa tayi tana dariya har da riƙe ciki ganin kamar ba namiji ba ya biyo su a guje nuna shi take tana zabga uwar dariya har da riƙe ciki,
biyota yayi ta shiga parlour mommy da gudu.
Bayan mommy ta shiga ta ɓoye tana danne dariyar ta mommy tace " juraij lafiya me ya faru..,
leko da kan'ta tayi tace " mommy gudun kadangare yake..,
sai ta ƙara fashewa da dariya har da buga cinya tana cewa namiji da gudun kadangare hhhhh wallahi mommy wannan abu ya ban dariya tare muka dinga gudu dashi yana ƙoƙarin rikoni wai kar mu tafi mu barsa.
a fusace Juraij ya zagaya bayan mommy zai fisgota ta dawo gabanta tana cewa wayyo Allah kinga akan na fadi gaskiya shi ne zai dake ni..
Haba juraij sai kace wani yaro ka dinga beye mata
Mommy ta faɗa tana danne dariyar ta , duk jarumtar juraij baya son ganin kadangare barin irin babban nan wanda har canza kala yake sabo da girma.
juyawa yayi bece komai ba .
ajiyar zuciya ta sauke ta zauna akan carpet tana sauke numfashi tuno ahlam tayi da ƙaton ciki tana cewa baby karka gudu ka barni dariya ta ƙara shekewa da ita tace " su baby manya..,
kallon ta mommy tayi tace " lafiya me ya faru kike magana ke kaɗai..?,
ba komai mommy
dauke kai tayi tace " dazu naje gurin mutumin nan da kika bani number sa , nayi bincike na tabbatar da gaskiya..,
da sauri ta ɗago cikin mamaki tace " mommy yaushe kika fita har wajen kenan kinje..?,
Eh naje yumna kuma yayi min bayani
gaban tane ya fadĩ karfa ya faɗa mata gaskiyar duk abin da ya faru da yadda tsarin su yake tace " mommy me yace miki wanne bayani yayi miki..,
gyara zama mommy tayi tace " yayi min bayani wanda ya gamshe ni saboda yace duk lokacin da mutum ya so dawowa yana iya dawowa sannan a guri me tsabta suke kai mutum wanda addinin sa ko imanin sa ba zai taɓu ba sai dai in mutum ne ya kaucewa dokar da suka shinfida mai amma su aiki suke yi da addini abin yayi min dad'i wallahi har ayoyi da hadisai yake karanto min mutumin masani ne kuma babban mutum wanda yasan kan'sa duk ya nuna min shedar kasar nan tasan da zaman su akwai sa hannun hukuma da dama ya nuna min..,
ajiyar zuciya ta sauke tace " to Allah dai ya dafa mana..,
amin ya Allah mommy tace ,
Bayan sallar isha ta shiga daki ta kwanta bacci me cike da jin dad'i har hango kan'ta take a makka.
Washegari
da asubar fari ta shirya kayanta ma tas ta haɗa su ta daure su a zanin atamfa wayar ta kuwa soke ta tayi ta saka a kugu
mommy ce ta shigo turus tayi ganin ikon Allah lamarin na yumna tamkar wacce aka jefe anya kuwa wannan abin da take yi lafiya qalau take
mutum yana cikin gatan sa yace sai yabar cikin gatan sa ya koma wata uwa duniya ta sani sarai ba yadda suka iya da ita shi ya saka suka barta kuma malam ma fushi yake da ita amma ko a jikin ta duk da be buɗa baki ya furta ba fuskarsa ta nuna abin da yake zuciyar sa ajiyar zuciya ta

sauke tace " yumna badai da safe zaku tashi ba..?,
cikin farin ciki tace " a'a ba da safe za mu tashi ba nice dai kawai na shirya domin kinsan jirgi baya jira sai dai a jira shi..,
hmmm Allah ya kyauta ta fadi haka zuciyar ta na mata wani irin suya Hajiyar su ma faɗa tayi tace a kyale ta duniya tafi bagaruwa iya jima tas zata koya mata hankali idan dai son abin duniya mutum zai yi to ba shakka zai girbi abin da ya shuka kuma zai halaka tana cikin wannan tunanin ne yumna tace " mommy wallahi saboda murna bazan iya cin abinci ba Allah ya sani ba ƙaramin farin ciki nake ciki ba " O,, Mamman yana nan yana figar talaucin sa ba damuwa idan na dawo zan bashi dan na jari...,
da sauri mommy ta kalle ta sai kuma tayi shiru domin bata da bakin magana juyawa tayi ta fita zama tayi a parlour zuciyar ta ba dad'i da ace juraij ya aure ta ba yadda za tayi dole ta zauna, ga maganar abokin sa da yayi mata ma lamarin babu shi domin ya koma gida hutu be kuma ƙara yi mata magana ba , Allah dai ya tsare rayuwar ta
mommy mommy mommy
da sauri ta ɗago tace " juhud har kin shirya yau da wuri haka..?,
zama juhud tayi tace " mommy tunanin me kike yi haka..?,
ba komai juhud
hmmm wallahi nasan ba zai wuce na yarinyar nan ba haka kurum kun dauki son duniya kun ɗora mata kun kasa hanta abin da tayi niya tun da tace sai tayi sai ku zuba mata ido gata ga hanya nan karta tsaya a makka ta , tafi bangon duniya wannan matsalar ita , ta shafa ni wallahi ko san ganinta ba nayi haka kurum ta jefe ki a cikin tunani kina ga ranar da malam ya bar gidan nan idon sa yayi jajir ko wannan hakkin da ta kwasa wallahi Allah ba zai barta ba

da sauri ta ɗaga mata hannu tace " juhud ya ishe ki, tafi bana son kara jin komai daga, gare ki..,
tashi tayi jikin ta a sanyaye tace " mommy Allah ya baki hakuri amma wallahi yarinyar nan..,
Cikin ƙara ji ta tari numfashin ta, tace " nace miki bana son jin komai daga, gare ki, ki tafi inda zaki Allah ya kiyaye hanya..,
juyawa tayi tana cewa amin..
dafa kan'ta mommy tayi ta lula duniyar tunani har lokaci yaja bata sani ba a guje yumna ta fito tana cewa mommy mommy mommy.
da sauri ta ɗago tace " yumna me ya faru..?,
cikin murna tace " yanzun nan aka bugo min waya, wai na zo za'a gama haɗawa mu ayi duk wani bincike da ake yi sannan sai mu tafi kin san fa muna da yawa..,
mommy tace " to bara salisu ya kai ki..,
a'a barni abin da gurin ba nisa ni daman na gama haɗa kaya yauwa idan kin yi waya da gida kice kina gaishe su jirgin mu ya tashi insha'Allahu duk wani kunci na rayuwar su zai zama tarihi idan na samu dama komai yayi dai-dai zan kira ku mu gaisa amma dan Allah kar wanda ya kirani ya taku ramin ina aikina kin san fa basa son Kiran waya wallahi idan na kirawo Na'ima dakyar take dagawa dan haka kar wanda ya kirani haka kurum su koreni su dawo dani niger ban tari abin arziki ba..,
salati mommy ta saki, amma ko a jikin yumna sai ma ƙara washe baki take dan ita bata ga abin aibun da tayi ba gaskiya ta fadi haka kurum ayi mata kutungwila ayi mata kafar kwaɗo su dawo

da ita Niger babu shiri.
shiga daki tayi ta fito da kayanta a ɗaure a zani ta ɗora su a kanta cikin washe baki tace " to mommy saduwar alkairi duk ki faɗa musu fa karki manta da ace ina Agadez da ko wanne gida sai nabi nayi musu sallama..,
Mommy ta dago da kyar saboda sarawar da kan'ta yake mata tace " Allah ya kiyaye hanya ya bada sa'a..,
cikin farin ciki tace " amin ya Allah..,
ta faɗa tana tafiya cikin farin ciki yau har wa'yanda bata yiwa magana a cikin gidan ta dinga bin su tana yi musu sallama so sai ma'aikatan gidan suke mamaki tsayawa tayi akan mati tace " to mati Allah ya kirani..,
da sauri ya ɗago ya dena gugar da yusrah ta bashi yace " ikon Allah mutuwa kenan za kiyi..,
wani kallo tayi mai na anya kuwa kana da hankali sannan tace " a'a lahira zan tafi ku shikkenan ba yiwa ɗan adam kyakkyawan zato sai ku zargi mutuwa dan nace Allah ya kira ni to ba wannan kiran nake nufi ba yau makka zan tafi duk wani bukata da kake da ita sai ka rubuta min a takarda domin muna sauka cewa zanyi akai ni harami na dafa ka'aba na roki Ubangiji..,
dariya ya fara yi har da riƙe ciki sanan yace " uhmm uhmmm yumna a ɗinga haɗawa da insha'Allahu..,
banza tai mai ta fara tafiya wayar ta ce taji tana ringing da sauri ta ciro ta , ta ajiye kayan ta a harabar kofar gidan nasu ɗagawa tayi tare da karawa a kunne tana cewa hello shamsiyya bana son bakar jaraba tun ba saba har kun fara kirana..,
shamsiyya tace " ke da hallacan wannan tafiyar da za kiyi bata gaba na wallahi tun da kin zaɓi bin yawon duniya da ki zauna gidan miji zaman bautar aure...,
kuttumar ubancan kayya sa lallai yau kin taɓo tsuliyar dodo dan ubanki ina ruwan ki da rayuwa ta kaga shegiya yar bakin ciki tafiya ce ba fashi sai na yi ta , muna sauka zan ce musu su kaini ka'aba na roki Ubangiji na haɗa da munafukai da yan hana ruwa gudu duk Ubangiji ya hana daku yayi maganganin ku shegiya me mutuwar zuciya ni an faɗa miki irin kice to buɗe kunnuwanki da kyau ki jini billahilazi wuwarramanu ko mamman be sake ni ba , sai na saka ya sake ni dan wallahi in har be sake ni ba sai na yanka mai ticket din tashin mutunci kala kala sai ya gwammace kiɗa da karatu dan uwar babanki
dan haka bara na fito mutu miki a mutum ni wannan sakin gaba takai ni kuma itama innar su hindatu zata ci jakar uban'ta wallahi na dawo sai na siya gidan su na saka an rushe shi,
Cikin yanayin zafin rai da fusata bakin malam har rawa yake bakin ciki ya tokare mai zuciya tari ya fara yana cewa yumna ko bayan raina karki sake ki dawo cikin gidan nan na yafewa duniya ke in har na isa da ke ki dawo ki zauna idan kuwa kika saka kafa kika tafi to wallahi ban yarda ba ki kara tako kafar ki cikin gida na da suwan kin dawo karya kike ki ɓata min suna, karya kike ki zubar min da mutunci na..
Inna hadiza tace " da kyau abin da tun farko ya kamata kayi kenan ka tsaya kai mata sako sako..,
runtsai ido yumna tayi ashe rashin  arziki shamsiyya ta shiyar mata hmm dai-dai take da su tace " malam tun farko fa kai kace na tafi kuma yanzu kace ba in da zani..,
Yumna in har na isa da ke to ki dawo ki zauna cikin yan uwanki..
to kawai tace ta kashe wayar ta mai dai ta inda take tana cewa wallahi ba wannan Maganar ko a kotu maganar farko ake dauka dan haka nayi nan munafukai ne suka zuga ka shegu masu

tafiya da lahira da ƙoƙon dambu sai naci kan uwar su a hannu a hankali zasu gane wace ce ni.
ɗaukan kayanta tayi ta ɗora akai ta ci gaba da tafiya tana zancen zuciya har ta isa lokacin tana shiga ana ƙoƙarin jera mutane a mota da sauri ta ƙarasa ta turmusa ta shiga zama tayi tana sauke ajiyar zuciya yumna nura da sauri ta ɗago cikin mamaki tace " lah Layla ashe kin zo..?,
dariya tayi tace " eh wallahi amma ki sauka kafin wancan ya gano ki ko baki ga saka mutane yake ba yana kiran serial number su...,
ke kyale sa wallahi naga guri ba in da zan sauka kina tunanin wannan uban yawon namu motar nan ba tai mana kaɗan ba ai wallahi kawai barsu salon ace sai gobe tun da har yau nayi sallama da kowa to bazan koma ko ina ba..,
Ke dan uwarki fito na saka kine taji muryar wanda yake jera mutane ya fadi haka da sauri ta juyo tace " me uwata tayi maka, ka zage ta haka kurum ina ma laifin kace min na fito sai ka zage ni..,
a fusace yace " zaki fito ko sai na fusgo ki tun kafin ki tafi kin fara mai da mana da magana ina da mun kai ki ai sai dai ki ce zaki dauki hannu ki dake mu..,
a fusace ta fito tana murguda mai baki sakar baki yayi yace " oga kallo yarinyar nan anya kuwa ba hakura za mu yi ba kaga tun yanzu neman fasa min baki take..,
wanda a ka kira da oga yace " muga visa ki..,
da sauri ta kunce kayan ta, ta ciro ta miƙa mai , amsa yayi ya gama dubawa yace " wannan ba a nan motar za a saka ta ba a can take...,
da sauri ta dauki kayan ta tabi wanda ya yi mata alama da ta bishi kara chanje kayanta su kayai sannan suka nuna mata gurin zaman ta ba dadewa motar su ta tashi a hankali ta fara tafiya har kuma ta hau titi ta soma gudu tamkar zata tashi sama ware ido sosai yumna tayi tana kallon garuruwa har suka zo filin tashin jirage nan ma ƙara duba su a kayi tare da yi musu rubutu a cikin visa su sosai yumna take baza ido domin ta ga layla amma na iya ba labarin'ta wata zuciyar tace to ko ba jirgi ɗaya za su hau ba ne.
bata da me bata wannan amsar a haka aka yi gama checking din su sannan aka basu set number su shiga yumna tayi tana kalle kalle zama tayi cikin farin ciki ina ma tana da babbar waya ta dauki kan'ta photo kallon matar kusa da ita tayi zata haife ta tace " ina kwana..,
matar da taci uban jambaki ga belching dena taunar chingum din'ta tayi ta fara kallon ta sama da ƙasa sannan tace " lafiya qalau ke daga ina kike..?,
murmushi tayi tace " yumna nura Agadez ni yar garin Agadez ce ..,
kai ta gyaɗa tace " oh kema kenan neman arziki kika fito da kananun shekarun ki..,
gyara zama tayi tace " aunty wa zai zauna yaga zama ai nima fitowa nayi a dama dani..,
dariya ta sheke da ita tace " ai kuwa kin yi kyan kai wallahi yanzu rayuwar nan idan baka tashi ka nema ba , to kana cikin takaici da bakin ciki dan wallahi wannan numfashin da muke shaƙa da ace a hannun dan adam yake to yasin wani hanaka shekar sa zai yi dan haka tashi mu nema ya zame mana dole ni kinga aurena na ballo na tawo haka kurum zan zauna ne ina cin garau garau mijina ga bakin talauci haka na tsallake ya'yana na ce na tafi nemo arziki..,
hmmmm aini dake kamar dan juma ne da dan jummai sai dai banbancin wasu abubuwan
da sauri ta kalle ta , ta miƙa mata hannu suka tafa tace " Masha Allah kenan zamu ce ta tarar tawo mu tafi ya akai aka haihu a ragaya..?,
limshe idon'ta tayi tace " labarin yana da tsayi amma zan baki shi tas..,
dariya ta sheƙe da ita lokacin kuma aka soma sanarwa jirgi zai tashi kowa ya saka belt tare da

kashe waya ko saka waya a play mode da sauri suka fara sakawa a hankali jirgin su ya fara tashi yana ƙoƙarin keta hazo dad'i ne ya kamata yumna tace " aunty na yarda da komai nufin Allah ne yau gamu a cikin jirgi wanda sai wane da wane suke shigar sa..,
dariya tayi tace " tabbas Allah ya nufa sai fatan dacewa da samun rahamar Allah...
haka ne wallahi ta faɗa tana kwantar da kanta a jikin kujera tare da kallon saman cikin jirgin.
wata mace ce ta soma zagawa ganin kaya a gaban yumna tace " ki ɗauke shi ki saka a loka..,
to tace ta tashi ta bude abin saman kan'ta daman taga mutane na sakawa amma tace ita gwara kayanta a kusa da ita yafi mata sauki haka kurum taje su zurare ta ƙasa ya za tayi da za ta saka idan taje can..
gama sakawa tayi ta komai ta zauna sosai suka dinga keta hazo har suka sauka gama saita kan'sa jirgin yayi suka fara fitowa zare ido yumna ta fara yi tana kallon wannan matar tace " aunty ya ban ga ka'aba ba , kamar wa'yannan mutanen ba larabawa ba kin gan su ba jallabiya sun ci ƙananan kaya..,
nima abin da na gani kenan amma ai larabawa suna saka kananun kaya suna cikin wannan maganar wani mutum ya ƙaraso yace " kune wa'yanda kuka tawo daga niger ko..,
kallon mamaki su kai mai ganin yayi hausa raɗau dukkan su kusan su ashirin suka ce eh mune. okay ku biyo ni.....
bin bayan sa su kayi, har suka isa wani guri wani mutumin ne sukai magana da matar nan da suka zauna guri ɗaya da yumna sannan ya tafi be kula ba ya ban gaje yumna da sauri yace " yi hakuri..,
yumna tace " bakomai wallahi,
sosai tayi mamakin jin yayi hausa kenan daman yan kasar makka akwai masu jin harshen hausa kenan
tana cikin wannan tunani ta dauko mata kayanta ya miko mata amsa tayi ya juya ya fara tafiya.
fara binciken su a kayi zuwa gurin yumna su kayi suna bincike kayan ta suka dauko wodar ibilis da wasu kayan maye..
nan danan gurin ya dauka jami'an tsaro suka hallara a gurin kuka ta fashe da shi   ganin an rutsa ta da bindiga,
ankwa wata yar sanda ta saka mata kuka ta fara yi domin bata san me tayi ba kallon aunty tayi da sauri matar ta matsa da ga gurin cikin Muryar kuka tace " wallahi ba abin da nayi me nayi..., bindiga wani ya saka mata a maƙoshi
wasu motoci ne suka shigo airport din a guje suka za gaye wa'yanda suka rutsa yumna buɗe motar wani yayi suka tura ta ciki kanta bugar glass din motar yayi hawaye na bin kuncinta sosai ta shiga cikin wani irin tashin hankali gashi ba damar yin magana duk sun rutsata da bindiga a kuje suka fita tamkar zasu tashi sama tare da yin jiniya kuka sosai yumna take yi ta shiga uku bata da kowa sai Allah Ubangiji ya zama gatan ta..

ba irin dana sanin da ba tayi ba tuni yunwar da , ta fara ji ta neme ta , ta rasa ba ƙaramin tashin hankali ta shiga ba lokacin da suka iso police tasion irin tsaron da ta gani ba ƙaramin guri aka kawo ta ba baza ta iya karanta komai ba domin rubutun da aka yi a bakin kofar gurin kamar larabci kamar ba larabci ba kan'ta ne ya ƙara juyewa ta shiga wani irin hali tusa ƙeyar ta su kayi da bindiga har suka shiga ciki a wani guri me raga aka ajiye ta zate ido ta fara ganin jami'an tsaro sai bincike suke yi a cikin wata computer wasu kuma na daga abin da ita tasan bata saka shi ba a cikin kayan ta ba suna rubutu a ciki da kuma wata takarda wasu ne suka ƙara fita.

duk sanyin gurin wani irin gume ne yake keto mata tun daga tsakiyar kan'ta.
a hankali ta furta ya Ubangiji ka fitar dani daga cikin wannan azzaluman mutanen..
hawaye na bin fuskar'ta zuciyar'ta tamkar zata faso kirjinta ta fito...

END OF BOOK 1

DOMIN SAMUN UPDATING BOOK,2
KU YI PAYMENT 500
8141785374 Amina alhasan Muhammad opay
Ku turo da shedar ku ta wannan number
08141785374
Yan niger kuma zaku turo ta my nita 1000fcfah
Idan ya zama complete document ya koma 1k ku hanzarta biya domin karanta ci gaba.